O[31/08, 16:16] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBA*

Creating and writing by

*Ummee* *Mukhtar*

🅿1

Iyayen tsaye suke akanta kamar zasu cinyeta d'anya saboda tsabar fad'an da suke mata " Iyee tsakani da Allah meye ai bun Alhaj Sa'id da har zakice bakya sonsa mijin da kowace mace zatai burun auransa ga kyau ga k'ud'i," kawai dan ya kasance kusan sa'an babanki sekice bakya saonsa?

Mahaifinne yai saurin cafe maganar da cewa kaji zancen banza zata dinga yawo da shine? Ke ki saura reni aure ba fashi jibi idan Allah ya kaimu in yaso ki had'iyi zuciya ki mutu .

Larai na gane yarinyar nan rufin asirin da Allah ya aiko mana dashi shi takewa bak'in ciki 'dan ubanki kamar bamu muka haife kiba.

Dubi yanda yase mana k'aton gida ga mota ya bani ga shagunan daya bani har biyu ga uban mak'udan kud'i ko yaushe akan hanya" amma ace Zarah kirasa wanda zakiwa bakin ciki se iyayenki.

Zarah wacce akewa fad'a ta kifa  kanta da jikin gado se kuka take na takaici da iyayenta suka kasance masu kakwad'ayin gaske"   tayama tana 'yar shekara 17  za abata dan shekara Arba'in da tara kawai danya kasance me kud'i?

Ta share hawayenta tana me goge face d'inta wacce tai ja saboda kuka.

Malam hadi ne ya sunkuyo kusa da Zarah murya  k'asa k'asa yace haba 'yata tinda mike baki ta6a bujirewa a binda mukace kiyi ba ' se akan wannan ?

Mun baki za6i daki kawo wanda kikeso kince yayi tafiya idan kin buga number sa batama shiga ,"ga wanna ya fito da k'arfinsa ze aureki, to Zarah zamusaki agaba kamar tv muna kallo ne?

Girgiza kai tayi Alamar a a ,  nan yai murmushi yace to yanda bazamu saki gaba muna kallo ba tobe kamata mun muki za6i kice ba hakaba.

Larai ce ta sunkuyo ta dafa kafad'arta tace ki hkr 'yata mun hango miki daular dake baki hango ba  , nan de    sukaita lalla6ata itako Zarah in banda sharar k'wallah ba abinda take wanda daga k'arshe tace ta yarda inde hakan ze sasu farinciki.

Nan  gaba  d'aya suka rungume ta suna sa mata Albarka itako taci gaba kuka .

Kwance take a d'aki tayi ruf da ciki idon yai ja sosai se kanta dake mata ciwo sosai , wayar ta jawo iphone7 tai dialing d'in wata number cikin kuka take magana Aysha ya zanyi ya zanyi Aysha kifad'amin se kuma kuka me tsuma zuciya.

Salati aysha tayi tace kiyi hkr gani nan zuwa yanzu.

Aje wayar tayi taci gaba da kuka .

Dake basu da nisa cikin minti 10 tak'araso gidan A tsakar gida ta tadda Larai wacce ke zaune tana shan farfesun kaji """ wani kallo taiwa Aysha na rashin kirki ,, cikin ladabi Aysha tace umma ina yini ",, fuska a daure ta amsa Åysha tai ciki tana mamakin sauyawar umman Zarah,,,, tinda 'yarsu ta had'u dame kud'i take d'aga kai.

Nan tai ciki umman Zarah ta bita da wani shegen kallo tace wallahi bazata yuwuba da anyi auran sena raba Zarah da wannan 'yar matsiyatan dan bazata goga mana talauciba.

Zarah na kwance Aysha ta shigo da sauri Zarah ta tashi da gudu ta rungume Aysha se kuka.

Subahanallahi Zarah dan Allah kibar kukan nan nasan de Akan Auran nan ne ki hkr ba yadda

zamiyi  haka Allah ya tsara.

Fuska taf da hawaye Zarah ta ɗago kai suna fukantar juna   tace Aysha taya zan auri babban mutun nifa yarinyace ,,,   babu wani so ko k'auna azuciyata game dashi """" ballan tana azo kan maganar shauk'i ta Auratayya nayi dashi nace nayi dawa ? Haba Aysha yaro se yarinya ni wallahi an cuceni  tai maganar tana me  kwantar da kanta akan cinyar Aysha....

Aysha tai ajiyar zuciya ta shafa kanta tace babu yanda zakiyi tunda sukace shi zaki aura kawai kiyi hakuri  bakisan Abinda Allah yake nufi da hakan ba.

Nanta d'ago ka cikin sauri tace a 'a Aysha ban hango  Alheri cikin auran nan ba sema tashin hankali.

A a don't  say that cewar Aysha ai sanin gaibu se Allah .

Batun shauk'i kuma wallahi wasu manyam sunfi yara iya soyaiya """"    Zarah tace au haka zakice?

Nan ta kama wani kukan da kyar aysha taita lallashinta akan cewa sanadiyyar biyaiyar dataiwa mahaifanta se Allah yasa abun ya zame mata Alkhairi.

Hira suka d'anyi wanda kusan rabi akan auranne wanda Zarah take cewa ita ba abunda zatai na harkar biki.

Ku biyoni yanzu aka fara😘

Ummulo
[31/08, 16:17] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBA*

*HIKIMA* *WRITTERS* *ASSO*🎁

Creatimg and written by

*Ummee* *Mukhtar*

🅿2

Misalin   k'arfe biyar na yamma   gidan ya cika da bak'i 'yan biki wad'anda sukazo daga k'auyensu wato cen dangin mahaifin Zarah """"   har yanzun tana d'aki wani ciwon kaine ke neman kamata  hayaniyar dataji tayi yawane yasa ta lek'o ta window nan taga mutane da yawa a farfajiyar gidan se farin ciki ake ",,wani guntun tsaki tayi ta koma ta kwanta tana cewa  duk akan Auran Babban mutun kukewa zumud'i aikin banza kawai ""

Jitai ana cewa ina Amaryar takene kota tafi gyaran jiki?

Larai tace wallahi tana ciki inaga bacci take"'   ke ni kuntuna mim ma yakamata da ace tayi gyaran jiki wallahi shaf na manta.

Wata wacce ake kira da maryam tace ah ai kinyi sakaci zaki  kai yarinya gidan kishiya  ace bazaki gyarata ba ?

Larai tai dariya tace ai gidan kowa daban ba abunda ze had'asu amma duk da hk zan gyarata duk da lokaci ya k'ure.

Su biyu suka  mik'e suka nufi d'akin Zarah, tana jin tafiyarsu tai saurin kwanciya azuwan bacci take.

Da sallama suka shigo baba maryam tace aiko bacci take yanaga idonta ya kumbura kode batada Ify ne ?  """"  d'ayar tace gashi ta rame sosai Larai meke damum 'yan nan ,::::   ?

Larai tai saurin cewa wallahi zazza6i ke damunta amma ai baza a fasa auran  ba saboda wannan.

Baba maryam tace yakamata  ata sheta"""

Tashinta sukai ta bud'e ido  a hankali kamar me bacci   cikin nutsuwa ta gaida su jikinta duk a sanyaye kamar wacce ruwa yaci.

Lafiya lau zarah kinci abinci kuwa?  Cewar baba maryam kai ta girgiza alamar bataci ba .

Ah maza Larai d'akko mata amarya ba cin abinci me a akai kenan """"   ta gefen ido Larai a kalleta gamida galla mata harara  wacce yasa Zarah saurin k'asa da kanta.

Abincin ta kawo mata sede ta kasa ci domin jitake yana mata d'aci spoon3   tai tace ta k'oshi .

Ba yadda basi ba amma takasa ci .

Ku kyaleta zataci anjima ne dama haka cin abincinta yake a tsintsnke.

Su baba maryan ne sukace ta tashi ta gyara taje gidansu kawarta su tafi gyaran jiki"" wani bak'in cikine ya zo mata wai ita wane irin gyaran jiki zataiwa wani tsoho.

Fita sukai daga dakin yayinda sukace tai sauri ta fito.

Laraice abaya ta juyo tace wallahi idan kika sake kowa ya fuskanci bason auran nan kikeba sena 6ata miki kebank'i ma na tsine mikiba tinda ba k'aunata kike ba Arzik'i na binki kina guje masa.

50k ta wurga mata tace gashinan daga cikin ku'din da Alhaj Sa'id ya bayar domin ki gyara jikin ki """ kinsan 150k yaba da to nasan wannan zasu isheki ,,da kallo Zarah ta bita yayinda Larai tai ficewarta .

Kuka Zarah tasa harda shure shuren k'afa tana cewa an cuceta.

Wanka tayi tasa riga da siket na atamfa se hijab ko kwalliya ba taiba tazo ta fice daga gidan babu wanda ta gani saboda duk suna daya bangaren.

Tafiya take amma kamar  bayi takeba saboda yanayin takunta shine ze tabbatar maka akwai a binda kedamunta .

Wata   majalisar samari tazo wucewa   suna ganinta sua hau nunata oh kaganta nan yarinya da ita amma wai tsoho zata aura sa an babanta .

D'ayan yai dariya yace eh mana Ai kasan ance kud'i hana magana idan  kanadashi balarabiya zaka iya aura    .    D'ayan yace kai wallahi kwadayi ma beba  suka kwashe da dariya.

Da gudu ta wuce su tana kuka ta fad'a gidansu Aysha  .

Aysha na tsakar gida umanta bata nan da sauri ta tasa kanta kan
K'afar aysha tana kuka.

Aysha  ta d'agota ce menene Zarah dan Allah kidena sa kanki a damuwa kada wani ciwon  ya kamaki.

Zarah cikin kuka tace kowama yasan Auran kwadayi za ' min Aysha ya bazanyi kukaba ?

Nan taita bata hkr akan komai mewuce wane .

Kud'in da ummanta taba ta tafi to dasu " Aysha ta dubi kudin tace wannan fa ?

Hawaye Zarah ta goge tace wai gyaran jiki zani kome zan gyara  oho.

'Yar dariya aysha tayi tace ah bari mu tashi muje  afara yau zuwa gobe shaken an kada lokaci ya k'ure duk da yariga yak'ure.

Harara Zarah ta watsa mata tace malama ba inda zani wallahi kawai na  fitone de dan kar ace banje ba.

Kallon ta Aysha tayi tace aike ko ba gyara wallahi da kyanki ko baki kwalliya kullun k'ara kyau kike musamman yanzu da kika samu Alhajin nan irin cimar dayake kawo muku gaba d'aya kin koma kamar wata shuwa Arab.

Ga rayuwa data sauya muku kun koma kamar damacen  kud'in masu kudine  ki godewa Allah.

Zarah batace komai ba se daga cen tace kawai ni kurkur zan ganbad'a ajiki da fuska shine zesa taga kamar naje .

Dariya sukai Aysha tace kin kawo shawara.

Nan suka had'a madara da kur kur se lemon tsamj kad'an wanda suka matsa ciki gaba daya suka shafa jiki da fuska .

Seda yai kamar 20mnts sannan suka wanke .

Wani suka had'a daban kurkurne da manja shima suka shafa daga baya suka wanke.

Sosai zarah ta k'ara haske damacen farace sol gata da gashi hanci kuma ga ido fari tas kamar madara.

Ba doguwa bace baza kuma a sata a sahun gaeru ba tanada jiki me kyan k'ira Allah ya hore mata mazaunai da dukiyar fulani dede misali wanda yake jan hankakin 'yan maza , .se d'an k'armin bakinta wanda aduk sanda take magana seya burge me kallo.

Aysha chocolate ce tanada kyau dede azanci.

Aysha kallon Zarah tai tace saura abu daya .

Tace me kenan? Aysha tace baki lalle ajiki ba duk da nasan jikinki damacen me laushine ga shinan ko a ido aka kalla.

Tsaki tayi tace bazan ba .

Dariya Aysha tai tace  wallahi  sekinyi so kike ta ramfoki baki jeba?

Zarah Tace kuma hakane fa.

Lallan   suka sa  a tasa nan ma sukazuba kurkur kadan suka juya suka dora a wuta minti biyu ya tafasa suka sauke suka zuba man zaitun sannan suka.shafa ajiki.

Ruwa me dumi Aysha ta dora Zarah ta fara shiga tai wanka """ bayan ta fito aysha ta  shiga.

Umman Aysha ce ta dawo suka gaisa da Zarah tana tsokanarta Amarya kinsaha kamshi.

Nan zarah tace zash tafi da aysha a gidansj zata kwana .

Tace ai bakomai kuje Allah yai muku albarka.

Ahanya Aysha tace kinga yanda  kika kara haske kamar gyaran jikin gaske kikaje?

'Yar dariya sukai nan Zarahta d'akko 30k daga cikin kudin ta bawa aysha .

Aysha tace mezanyi da wannan ?  Zarah tace baki nai " ni kuma?   Cewar aysha ai ban ta6a rik'e irin wannan kudin ba  ko ummata bata da wannan kud'in.

Zarah tace shiyasa na baki kuma umman ma zan bata  nata   kinga ko jari kwaja tinda mahaifinki ya rasu Aysha.

Rungume juna sukai Aysha na kuka tanai mata godiya.

Suna shiga gidan kai tsaye d'akin Zarah suka wuce dan ita  bataso ma kowa ya ganta.

Ummulo😘😘😘😘
[31/08, 16:19] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBA*

Creating and Writting by

*Ummee* *Mukhtar*

*HIKIMA* *WRTS* *ASSO*🎁

*SADAUKARWA* *GA* *DUKKAN* *MASOYA* *WANNAN* *NOVEL* *ALLAH* *YABAR* *ZUMUNCI🤗😘*

🅿3

Suna shiga d'aki zama sukai a kujerun dake d'akin suna kallon juna gamida murmushi Aysha tace Allah yasa de kada umma ta gane bamu jeba """"" Zarah ta cire hijab gamida warware dogon gashinta wanda ya zuba har baya ta zauna kusa da Aysha tace karki damu bazata ganeba .

Wata jaka ta dakko dake cikin drower ta zuge kud'ine a ciki fal wanda zasukai kimanin dibu d'ari uku da hamsin Aysha tai saurin zare ido """" tace ke wannan kud'in fa ?

Wani dan guntun smile Zarah tayi gamida yin tagumi tace zaki d'auki dukansu ki kaiwa ummanki """ Aysha tace wa? Rufamin asiri ai in aka ganni da wannan kud'in cewa za ai mutun na siyar nasame Su.

Dariya Zarah tayi wacce rabon datayi irinta harta manta domin yanzu bak'in ciki ne lullu6e a zuciyarta gameda Auran nan .

Tace ok ni zan kai mata da kaina amma ko kin manta mutumin nan d'an siyasane yana daya daga cikin masu baiwa shugaban k'asa shawara kin tina?

Aysha ta gyad'a kai tace hakane.

Zarah tace to su kud'i ba wani abu bane a gunsu dan haka kema kici naki rabon domin kuwa kud'immune .

Dariya sukai Aysha tace gaskiya zakiji dad'i 'yan nan wannan idan kikai wata daya nazo gidanki wallahi zan iya kuwa ganeki?

Duka Zarah takai mata tace eh saboda kinsan zan koma kamar dodo ko?

Nan Aysha tace no ba haka nake nufiba zade ki k'ara kyaune hajiyata.

Suna cikin magana Larai ta shigo kafin tai magana se taga Zarah k'ara wani haske da kyau""" fuska a sake tace kai masha Allah kin ganki kuwa nagode miki 'yata ai shima ya dad'a ganinki da kyau.

Motsi Zarah takamayi da bakinta Alamar tana k'unk'uni domin ta tsani taji an had'ata da Alhaj Sa'id.

Nan ta juya kan Aysha tai mata wani kallo na raini tace au kema gyaran jkin kikayi ?

Cikin sanyin murya Aysha tace eh umma.

Baki Larai ta ta6e ta kalli Zarah fuska a tamke tace kinajina gara ki k'ara gogewa da wayewa domin nan gaba kad'an zakifara mu amala da matan masu kudi gogaggun matan 'yan siyasa to karki da wasa nide nagayamiki .

Zata fita kenan ta k'ara juyowa ta harari Aysha kad'an tace ni yaye yayene banaso kowa ya tsaya iya matsayinsa daga hk tai waje taja musu k'ofa.

Zarah kallon aysha tayi tace pls kiyi hkr dan Allah nasan dake take "   ta manta cewa muma da haka muke ba shine da muba .

Murmushi aysha ta k'ak'aro tace ke kinji ki waya gayamiki dani take kawai fa tana miki baya nine idan kinyi aure kema  zaki shiga a dama dake.

Uhmm Zarah tace da Aysha  tace kede kawai kin waskene amma dan Allah kiyi hkr .

Dan Allah meye hk banaso na fad'a miki ba dani takeba.

Yauwa wai wane kayan zakisane ran d'aurin aure   anya ma kinyi gayya naga ba wata k'awa da muka gayyata?

Baki ta ta6e tace aysha dan Allah dan Annabi  idan kinason farin cikina kidena min maganar komai akan auran nan dan Allah.

Tsaye aysha ta mike tana me shirin  shiga toilet d'in dake d'akin danyin wanka " tace yanzj hk za

ai auran kamar wani auran bazawara ?

Naga zaurawamma na yanzu idan kikaje bikinsu wallahi seki rantse bikin budurwa kikaje.

Amma tinda kince a barshi ba komai.

Daga hk ta shiga toilet.

Cuno baki Zarah tayi tace lalle ma Aysha dama saurayi zan aura shine zanyi wannan gwad'aren amma ba wannan ba daga tai kwanciyarta a kan gado.

Ba yan ta fito daga wanka Zarah itama ta shiga tai nata wankan gamida d'orawa da Alwala.

Seda akai ish'sha sannan sukai shirin kwanciya bayan an kawo musu abinci me rai da lafiya.

Zarah gwanace wajen yin chart da hakane tai abokai da yawa maza da mata "" Amma komai mutuncinka da ita da zarar kace kana sonta zatai blocking d'inka .

Yanzu ma wayarce rik'e a hannunta se faman latse latse take.

Aysha tace nima gobe idan mun fita waya zan siya nima na shigo gari """   'yar dariya Zarah tayi tace karki damu goben idan Allah ya kaimu semuje cen berud road musiyo ko?

Aysha fara'a tai tace Zara kimmin komai bansan dame zan saka mikiba .

Juyowa Zarah tai tace kinsan dame zaki sakamin?

Girgiza kai Aysha tayi zarah ta tashi zaune tace to sonake kidena cewa nai abunda zesa kowa yasan inason auran nan kawai kija bakinki kiyi shir,,,,,,,,,,,,,
Ai kafin tak'arasa  Aysha ta kwashe da dariya  tace ok tona dena

Mintsininta Zarah tayi cikin wasa Aysha tace Allah zesakamin  Zarah tace yasakama na tare.

Dariya sukai me isarsu""sunata hira har wajen k'arfe 11 sannan sukai addu'ar kwaciyar bacci kowanensu yaiwa d'an uwansa seda safe.

Kyakyawan matashine wanda kallo d'aya zakai masa katabbatar da cewa shid'in daga gidan hutu ya fito duba ga fatar jikinsa zuwa kayan dake jikinsa .

Kallo d'aya zakai masa kasan shid'in sun had'ajini da shuwa Arab""  ya had'u sosai dogone

amma ba cenba farine sosai kamar balarabe haka sumar dake kansa bak'ace wuluk wacce ta kwanta luf akansa"""" kana kallon idonsa zakaga har wani walwali yake kamar gwal"

Yanada hanci dogo se matsakai cin baki.

K'irjinsa kwance yake da gashi kamar na india wa wanda yake tafiyar da hankalin 'yam mata .

'Yam mata basu da meshi ba ko kad'an sede su suke kawo kansu gareshi da k'ok'on barar soyaiya koma ya aure su.

Hakan baya gabansa domin shi har yanzu bega macen datai masaba.

Mata da yawa kan nemi shi koda kwanciya ce yayi dasu koda be aure suba Amma shid'in mugun miskiline ba kuma ya fasik'anci ko Alfasha.

Sanye yake da jar T shirt se bak'in 3quter wanda ya baiyanar da sumar dake kwance a k'afarsa ta kwanta a dukkan jikinsa.

Wasu turawa ne biye dashi a bayansa rik'e da wata box wanda suke d'auke da muhiman

papers aciki  wanda ake gudanarda harkar cinikayya tsakaninsu da wasu daga cikin companin dake k'asar ta Switzerland.

Wani bene suka hau yayinda suka danna lifter tai sama dasu seda sukaje har wani  guri megirman gaske sannan suka bashi box d'in ya shiga ciki ya d'akko musu wata box d'in sannan sukai sallama suka juya.

Yana shiga kai tsaye toilet ya shiga yai wanka wanda fad'ar had'uwar toilet d'in 6ata lokacine.

Komai na d'akin a don golden ne   nan ya fito sanye da tawul yana goge jikinsa lokaci lokaci yana d'an tsaki .

Seda ya 6ata time a gurin shafa mayukan dake zube akan mirror kamar wata mace sannan daga k'arshe yasa singlet da wani 3quter  amma dukansu white ne sannan ya haye bisa makeken gadon.

Phone d'insa yad'akko yana k'ok'arin had'a wasu numbers alamun yayi missing number dayake son kira.

Zarah  misalin 12 na dare bacci take sosai taji phone d'inta ya d'auki ruri .

Cikin lalube takai hannu ta d'akko idanuwanta duk a rufe tai picking call cikin muryar bacci tace hello """"    daga d'aya bangaren yace ina magana da wace?

Turo baki tayi duk da hk idonta a rufe tace oho kai daka kira bakasan waka kiraba ?

Cire phone d'in yayi daga kunnensa ya k'ara kallon phone d'in "   yace am sorry   dan Allah ba momy bace?

Cikin tsiwa Zarah tace ah kakace  " dariya taso kamashi amma ya daure beba yana dad'a saura ranta. zaune ta tashi itama tana kallon number da alamu ta k'asar waje ce towa suke dashi a k'asar waje?

Taiwa kanta wannan tambayar.

Tace ko bakajiba ok kaima kasan BABBAN MUTUN zan aura shine kakirani kaci min mutinci?

Katseta yai yace kiyi hakuri wallahi momy na nakeson kira inaga ba dede nasa number bane but am so sorry.

Tsaki tayi tace to wannan baby ka kira ba momy ba d'if ta kashe wayar gaba d'ayanta tai cilli da ita gamida komawa bacci.

sosai yarinyar ta bashi dariya kalamanta duk na k'uruciya ne zeso yaga yarinyar nan azahiri""" Haka nan ya tsinci kansa cikin farin ciki dajin muryar wannan yarinyar dabema san sunan taba.

Seda ya had'a number wajen so 3 yana kira amma ba wacce yake nema bane.

Harya hkr ya k'ara gwadawa cikin ikon Allah number momy ta shiga.

Zaune take kan dadduma da casbaha a hannunta tanaja taga kiran sa.

Da sauri ta d'aga dan ko ba a fad'a ba tasan k'anin natane .

tana d'agawa tace kaiko MUSAYYIT anya Ify kuwa yau sati 2 data fiyarka ba kira ba d'aga hannu?

Dariya yai yace am sorry momy wlh na yarda duka sim dina ne kuma kinsan bana haddace number waya shine dalili wannan ma dakyar na had'a ma kira bayan nase wani layin amma amin afuwa.

Murmushi tayi tace Musayyit sarkin shiririta to da ftn ka gama komai kasan Auran Abbanka ya kusa """" seda yai jim sannan yace to momy insha Allah jibi ina hanyar dawo wa kitana di kayan dad'i dariya tayi tace bazan ba inkayi zuciya kai aure.

Murmushi yayi yace inna dawo akwai labari .

tace da gaske ?

Yace Allah momy daga haka seda suka dauki tsawon awa daya suna hira daga k'arshe sukai sallama.

Kwanciya yayi yana murmushi yana tina hirar da sukai da yarinyar dabe santaba gashi tana nema tazauna a zuciyarsa.

kalma d'ata tak ya tuno da take cewa kaima kasan BABBAN MUTUN zaura shine ka bugo kamin rashin mutunci.

Tsam ya mik'e tsaye yana zagaye tafkeken d'akin zuciyarsa na masa wani iri wandabe san komeye ba.

kubiyoni dan jin yazatakasance tsakanin MUSAYYIT DA ZARAH

Shin musayyit kode d'an Alhaj sa'id ne?

ummulo ce taku har kullun🤗🤗😘
[31/08, 16:19] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBAN*
*MUTUM*

Creating And Written by

*Ummee* *Mukhtar*

*HIKIMA* *WRTS* *ASOO*🎁

🅿 4

A subar fari mutan gidan suka tashi dan gabatar da sallar Asbah bayan sunyi ne wasu daga ciki suka koma bacci " yayin da wasu suka zauna zaman hira .

Zarah da Aysha tin 4:30 suka tashi suka zauna suna hira bayan sunyi sallar Asbah ne suka koma bacci.

Misalin 7:00 kiran a wayar Zarah ya fara ruri yayinda suketa bacci abunsu.

Aysha ce ta farka ta d'aka mata duka tace tashi inaga Angon ne ke kirah """   Mik'a Zarah tayi ha'd'i da salati tana mutsitstsika ido tace yanzu akan wannan kike tashi na ?

Wama ya fad'a miki yanada lokaci na mutum kullun a tafiye tafiye daga wannan k'asa zuwa wannan k'asa "   kai ta mayar ta kwata gamida yara pillow tana cuno baki.

Haka wayar ta gama ruri " Aysha na shirin  kwanciya ta kuma jin wani kiran ya shigo tashi aysha tayi ta jawo phone d'in setaga number amma ba suna d'agawa tai gamida sallama .

Kwance yake a d'aya daga cikin sofa d'in dake palourn hannunsa rik'e da cup na green tea yana sha kad'an kad'an aje cup d'in yayi   yace mrng  funny gal   how are u anda how was ur Ist 9t?   Aysha k'unshe bak'i tayi tanaso tai dariya cire phone d'in tayi tana k'ara duban wayar """ am sorry barina tashe ta bacci take me wayar .

Tsaye ya mik'e yace no karki tashe ta batta tai baccinta amma pls idan ta tashi ko plashing ne kimin kinji dan Allah.

Da sauri tace to to  .

Kashe phone din yayi ya kama had'a mahimman kayaiya kinsa domin yau yakeson tafiyama tinda  yariga daya kammala komai daya kawo shi.

Mamaki aysha take waye to wannan kode kabeer ne wanda ya tafi da har yanzu bedawo ba?

Tace kai bashi bane wannan muryar sa kamar ma ta larabawa ba haka voice d'in kaber takeba.

Kwanciya tayi abunta gamida aje wayar akan table.

Ta kwas dede suka farka a time d'inne suka fito dan kar6ar breakfast.

Kitchen  suka nufa da kansu suka hada komai suka koma d'aki.

Bayan sun karya wanka sukai suka fice yayin da Zarah ta d'auki jakarta wacce take d'auke da kud'i.

Aysha tace muje mugaisa dasu mana kafin mu fita "Zarah cewa tai ita ba inda zata kawai tataho su tafi.

Kai tsaye gidansu aysha sukaje umma suka samu tsakar gida se a lokacin take dama koko.

Har k'asa suka gaidata ta amsa cike da fara 'a tace a a kune da wuri hk?

Eh umma  zami dilkane shiyasa kuma zamuje gyaran gashi.

Oh ai gara kuje da wuri ai tinda gobe ne d'aurin Aure .nan da nan idon Zarah ya cika da k'wallah aysha nakallonta dan hk taja hannunta sukai ciki.

Haba Zarah dan Allah kidena sa damuwa bakisan abinda Allah yk nufi da Auran nan ba amma duk kinbi kim damu "nasani da ciwo ba dad'i domin ba kalar mijin da kike mafarkin samu zaki aura ba amma kisani cewa komai muk'addari ne ke kuma hk taki tazo miki pls kisawa ranki ruwan sanyi.

Se sannan k'wallah ta zubo mata tace bakomai ya wuce na dena k'awata.

Dake basa rabo da kayan gyran jiki a a jiye nan da nan ska had'a komai suka koma wani d'akin na daban suka fara.

Seda sukaci abincin rana sukai wanka sanna sukai shirin tafiya saloon.

Umma na zaune tana jin 'yar redion ta zarah ta tsuguna gabanta tace gashi umma .

Da murmushi umma tace meye wannan d'in kuma?

Jakar ta zuge nan taga kud'i fal ta rufe baki tace ke ina kika samo wannan?

'Yar dariya zarah tayi tace umma karkice komai dan Allah na kine kena bawa kıyi duk abinda kikeso dasu dama kin dad'e umma kina neman jari to gashi Allah ya kawo miki kema kici

k'udinki.

Kallonta umma tayi aysha na tsaye se murmushi take kawai" umma cikin rawar baki da sanyin murya tace kamar ya naci kudina zarah
?

Eh umma ai kud'immu ne suke hawa kai suyi d'are d'are akai sbd haka dan Allah karma kifad'awa umma na dan bata sani ba wannan daga cikinirin kudin dayake banine.

Kuka umma tasa sosai ta rungume zarah tace Allah yai miki Albarka Allah yabaki abinda kikeso ngd ngd zarah """ kuka take sosai zarah ta goge kwallar data tarar mata tace umma zamu tafi se gobe zamu dawo cikin sauri umma tace to to zarah nima inason naje yanzu zan tashi to kawai sukacs suka fice.

Nan suka bar umma se kukan dad'i take domin ko 50k bata ta6a rikewa ba.

Suna fita aysha tai taiwa zarah godiya.

Kai tsaye berud road sukaje aysah tase waya babba HTC ta siya tase sabon sim na glo .

Umma shiryawa tai taje gidansu zarah amma ba wata tarbar kirki da larai tai mata dama ta zone ko akwai aikin daza ayi.

Wajen saloon sukaje wanda se karfe shida suka bar gun suka wuce gida.

Tj multi pps sukaje kaya tasewa aysha na musamman d'in kakku masu tsadar gaske.

A gajiye suka dawo nan suka tarar da mutane sunfi na jiya domin wasu sunzo daga cen garin ummanta """" fuska tamke zarah take gai da kowa yayinda aysha fuskarta ke sake se tsokanarta suke amarya kinsha kamshi.

Wani haushi ne ke kamata mustu mutsu kawai take da mouth d'inta wanda da alamu so take tai magana .

Larai ce ta watsa mata uwar harara hannun aysah taja sukai ciki.

Suna zuwa suka taradda abinci an aje musu.

Kaya suka cire yayinda zarah ta dakko musu marasa nawi daga ciki kayanta .

Abincin sukaci kad'an saboda har yanzu akoshe suke.

Larai ce ta shigo ita a baba maryam hannunsu rike da wasu flaks har biyu .

Da murmushi larai tace amma fa kinyi kyau wane gum gyaran jikin kikaje dan na san anja kud'i da yawa gashi daga farawa tsakanin jiya da yau har kin kara fresh dake.

Da sauri zarah tace um cen beautiful bride mukaje .

Ah koda naji ai dama sun iya sa fatar amarya kyau da shek'i " toga wannan kicinye duka kinajina ko?

Eh umma kawai tace baba maryam tace wannan zaki faraci shine na kaza wannan kuma na auran shila ne ki daure ki cinye za a akawo miki sauran na shane seki shanye abune anyi shi a k'urace .

Kallon juna sukai zarah da aysha.

Fita su larai sukai sukaja musu k'ofa.

Wallahi bazan ciba se kace wani saurayi zan aura cewar zarah"""" ' yar dariya aysha tayi tace ki daurw kici kinga nasan musamman aka yishi sbd ke .

Zarah tace sede muci tare "zare ido aysha tayi tace rufamin asiri wace ni .

Leda zarah ta samu ta juye komai a ciki na abinda aka kawo mata tasa hijab ta fita .

Ina zaki kuma cewar aysha ke k'yaleni kede kisa ido .

Da sand'a ta fita ta zaga ta baya ta wulla akwandon shara.

Dariya ta shigo tanayi ta cire hijab tace nasa a shara """".baki aysha ta bud'e tace shame? Zarah tace shara ai kinjini .

Dariya aysha tayi tace to Allah ya kyauta.

Yanzu idan akagani fa? Cewar aysha, zarah tace Bama wanda zegani .

Au na manta wlh d'azu da safe wani ya kira wallai bakiji muryar sa ba kamar arab gaskiya ko ban ganshi ba duk inda yake nasan ya had'u.

Zarah d'aga kai tayi sama alamar tinani cen tace oh jiya ma kira wai momh yake nema niko nace masa wannan baby ce.
Kawai ina bacci na nake gayamiki mutumin nan ya kira ni wai wani dawa nake magana.

Ya ban haushi wlh.

Aysha tace kinsamme wlh duk yadda akai sonki ma yake cewa yaifa kina ina nace bacci kike amma yace waina kyaleki kisha baccinki karna tasheki idan kin farka nakirashi ni kuma sam na manta.

Zarah tace uhmmm kyale shi irin masu had'an number nanne idan sunyi sa'a sunsamu mace shi kenanse suce suna sonta.

aysha kayya banajin wannan irinsu ne gaskiya .

Hmmm zarah tace kawai zata mik'e kenan kiran wayar Alhaj sa'id ya shigo tana gani ta Kashe phone d'in gaa d'aya tasa ajakarta.

Aysha batace komai ba tana shan juice sede murmushi kawai datake kawai.

Seda sukai sallah sukai shirin kwanciya idonsj biyu amma hira suke  aysha tace shikenan fa dg gobe angama .

Uhmm kawai zarah tace ina jiyewa bawan Allan nan rashin mutuncin da zan shuka masa wallahi da kansa seya sakeni se yayi dana sanin aurena .

Ah karki haka kawata in kikai hk kenan  baki dauki shawarata ba kenan idan kikai haka baki kyauta ba.

Hakuri shine maganain komai fa .

Juya kai zarah tayi hawaye na bin kuncinta gamida rufe ido.

Musayyit zaune a cikin jirgi ji yake zuciyarsa na masa ba dad'i meyasa har yanzu yake jin wani abu a zuciyarsa gameda wannan yarinyar amma koma menene daya sauka ze nemi inda take murmushi yayi ya maida glass d'in dake face d'insa ya shafi sajensa wanda ya kwanta a kyakyawar fuskarsa.

Wata baturiya ce ke yawo tana raba irin abincinsu wanda ya k'awatu da ganyaiyaki kala kala " nan tazo dede gun musayyit ta aje masa a k'aramin table amma yaceta d'auke ya k'oshi.

Farin cikine kawai a ransa wanda besan dalili ba lokaci lokaci yana tina fuuny gal d'insa.

Ummulo😘🤗
[31/08, 16:19] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* **BABBAN*MUTUM*

Creating and Writting
By
UMMEE MUKHTAR🎁

🅿5

ABUJA

Wani katafaran gida wanda komai k'urin lakka bazaka iya gano ina ne k'arshen gidan ba saboda tsabar nisan gidan , koda ka shiga haka zakaita wuce wurare tamkar ka shiga wata unguwa me nisan gaske.

Gidan gaba d'aya zagaye yake da ma aikata wanda suka had'a da security's and bodyguards, sojoji masu uniform da marassa uniform.

Wani bangare dg cikin gidan na hango wanda da alama anan mamallakin gidan matarsa take.

A time din karfe 10am"""  palour agidan da d'akuna kamar kamar zasuyi magana sabod yawansu.

Ko wane palour adonsa da banne ko ina akwai kayan kallo firij dining area A.C.  da sauransu.

Kowane daki akwai gado toilet 3chairs  karamin center na glass kayan make up da sauransu yanayin gidan kai ka rasntse a hotel kake saboda yawan gurare wanda duk inda ka kalla se sun tafiyar da hankalinka sbd kyau da tsaruwa.

Ga mata nan masu aiki kowacce da uniform white shirt and red jeans.

Fulawo yi ko ba a magana gasunan se rangaji suke suna fitarda kamshi.

Wasu manyan maza nagani kaida ganinsu kasan sunci suntada kai  duba ga yanayinsu da kuma kayan Alfarmar dake jikinsu.

Wani mutun na hango fari ne sosai sanye yk da farar shadda wacce kudinta idan aka fada zakai matukar mamaki agogon dk hannunsa ma kaida gani kasan yaja kudi.

Yanada kyau sosai kamar kata6ashi jini a fito sede kana kallonsa zaka gano shekarunsa duba da yanda furfura ta fara futo masa kadan kadan.

Hira suke cikn harshen turanci wanda a time din suke shirin tafiya daurin aure"""

Wata mata nagani dauke da turare a a hannunta se fara 'a take da alama itace matar gidan " tana zuwa ta fesawa Alhaj sa'id ,""  Abokan nasa kuwa dariya sukai ciki tsokana suke cewa ah lalle kin cancaci kyauta  madallah da matar Arziki irinki '   dan murmushi tayi ta gaidasu yayinda Alhaj sa id wata kunya takamashi domin yana matukar ganin darajarta domin tayi masa halacci arayuwa.

Kudi suka hau aje mata dami dami tin tana godiya har tai shiru se murmushi kawai tk.

Fita sukai dukkaninsu Alhaj Sa'id ya sumbaceta  gamida shafar fiskarta yace semun dawo ko.

Kai kawai ta d'aga masa harya fice yayinda   hawaye kebin fuskarta.

Da sauri ta share fuskarta ta koma inda 'yan uwanta suke wanda sukazo jiya domin biki.

Suna fita motacine masu yawan gaske ko wacce da driver nan suka shiga se filin jirgi.

Zarah zarah wai dan ubanki har yanzu me kikeyine a d'aki daurin auran nan kinsan fa shad'aya da rabine shine bazaki fito ki gyara jikinki kiyi kwalliya ba?.   Cewar Larai.

Ah k'ila gyarawa suke kinsan kwalliyar yaran nan ta zamani bare su zainab da hafsat ga sunan duk sunzo d'azun zasu gyarane """" baba maryam ce ke maganar.

Am wai yanaga ba a d'ora komai ba ne ko tukwane banga an d'oraba ?

Larai tai murmushi tace ai order na bada kinsan yanzu in kanadashi base kasha wahalar komai ba ai tun bikin saura sati d'aya na bada kud'i ayo sede kawai kiga an kawo nan da anjima zakigan su ' kawo da ranama zasu kawo wani.

Eh lalle shiyasa naga wlh banga tukunya ba to kinga ai muma hutummune " Ah to cewar wata dake shirin shiga toilet wanka.

Zarah na kwance a d'aki se kuka take jikinta ya d'auki zafi aysha se lallashinta takeyi akan tai shiru amma tak'i

Sauran 'yam matanne wanda zasu kai su biyar wanda duk 'ya'yan 'yan uwane domin zarah ba wanda ta gayyata suma hakurin suke bata amma kamar tirata suke.

Shigowar Larai kawai suka gani hannunta d'auke da wayar caja se huci take """ Zarah na ganin ta ta mik'e tana jan k'afarta zuwa jikin bango.

Larai tace wuce muje muje nace ko"""" zarah kuka take sosai tana cewa ammi dan Allah kiyi hkr """" mari Larai ta d'aukr zarah dashi wanda seda aysha taji kamar ita aka mara ta rintse idonu .

Jan hannuta tayi ta cillata toilet d'in dake d'akin tace ai ba wanka kika wuce nai miki ba so kike kitsinkan mutunci kuma wallahi baki isaba .

Aysha cikin tsoro tace Ammi kiyi hakuri zatayi """   kallon banza  Larai tayiwa aysha tace ke rufemun baki 'yar karere nayi magana dake ?  Waya samma koke kike hure mata kunne saboda kinga zatashiga daula "irinku nada yawa adoran k'asa na sani kawai fitowane da bazaki ki nuna ba se zagon k'asa  zaki fara wankan ke kuma kose na danno k'ofar nan .

Zarah tafi jin bak'in cikin kalaman da Larai ta fad'awa aminiyarta me lallashinta kuma mebkaunarta Akan wankan da akasata setayi.

Aysha kanta na k'asa tana wasa ta farcenta yayinda ta hadiyi yawu na takaici.

Larai kanta tsaye ta shiga tafara wanke zarah sosai itako se kuka take abinta .

Sauran yan matan suma basujj dadiba duk fita sukai farfajiyar gidan suka zauna.

Wanka suma suka yi yayinda suka shiga fesa kwalliya.

K'ofar gidansu zarah cike yake da 'yan d'aurin aure kowa ka gani cikin farin ciki domin kowa ma murnar zeyi tozali da matemakin shugaban k'asa.

Malam Hadi anci shadda gezna fara kana kallonsa kasan a farin ciki yake,

Jiniya suka faraji yayinda kallo ya koma kan hanyar wacce da sassafe mlm hadi yasa aka share layin kaf dinsa aka kafa runfuna.

Nan Manyan k'usoshin gobnati suka fara fitowa kama daka kan ministoci 'yan majilasu govnoni da kuma manyan ma'aikata.

Malam hadi da sauri ya nufesu se washe baki yake yana cewa sannunku da zuwa mutane nan aka shiga hotuna unguwar gaba d'aya tacika da jiniya sojoji rik'e da bindugu kamar za a fita yak'i.

Alhaj Sa'id da murmushi yabawa ml hadj hannu sukai mufabaha hannun mlm hadi se rawa yake dan murna da zumud'i.

Nan suka zazzauna a inda aka tanada don d'aura auran .wayarsa ya ciro wacce se walwali take yaiwa zarah tex kamar hk.

My baby ina ftn kina lfy yau Allah ze cika mana burimmu
I love you .

Nan ya kashe phone din gaba daya aka shiga daurin aure mutane se hotuna suke.

Zarah na zaune fuskarta tai ja daure da tawul ajikinta iya cinya se kuka take k'asa k'asa Larai ce dasauran 'yn uwanta se lallashinta suke akan ta daure tai kwalliya me kyau aysha na gefenta

tace wa Larai Ammi  zami mata yanzu .

Larai kallan aysha tayi  tadanyi fara'ah dake tasan zata gyara mata 'yarta tace to ku daure ayimata da wuri gasucen sunzo.

Fita sukai sy larai aysha ta rufo kofa tazo suka fara gyara zarah Abun mamaki gani sukai kawai ta tsaya ta dena kukan se ajiyar zuciya datake yi.

Daga waje sukaji ance an daura auran Auran Alhaj Sa'id wati vise president da Zarah Habib Akan sadaki naira million 10 .nan aka d'auki tafi yayinda wasu ke mamakin adadin sadakinta .

Malam hadi kamar ya suma dan dadi  jiyake kamar yafi kowa sa'ar haihuwa.

Zarah najin haka ta rik'e kanta wanda ke juyawa ta runtse idonta se kuka  kwanciya tayi tana burgimase shure shurw take su Aysha da hafsat na rik'eta.

Larai kuwa wata uwar gud'a ta rangad'a ita da matan gidan se barka suke wa juna sunfita zakkah a dangi.

12 dede MUSAYYIT  ya sauka a Airport  fuskarsa dauke da fara'a nan naga mutane sun baibayeshi suna masa barka da zuwa yana amsawa cike da kulawa yana raba musu kudi""" hak yake aduk sanda yai tafiya ya dawo dake sun saba da ma aikatan haka zeta basu kudi kamar banza.

Wani ne yace yalla6ai zamu kaika ne ko kuwa kayi waya gidane ?  Musayyit  ya cire farin glass din dk face dinsa yace no kaini kawai zakuyi inaso naiwa momy na surprise ne.

Murmushi sukai dukkan ninsu sukace girman kane yalla6ai.

Phone dinsa ya ciro kai tsaye layin Zarah ya fara kira wacce yai mata saving da funny gal Amma a kashe   so 5 yana bugawa amma shiru.

Suit d'insa ta saman naga ya cire yana furzar da iska alamar beji dad'in hakan ba.  Yaso ya fara jin muryarta domin itace a zuciyarsa amma hakan be yuwuba.

Wayar Dad ya buga itama akashe kallonsa yai yace we can go """ nan  wata mota ta parka me d'an banzan kyau  suka d'auki hanyar gida.

Ummulo ce taku     inasonku masoya wannan novel😘👄💞👍🏻
[31/08, 16:19] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBAN*
*MUTUN*

Creating and written
By

UMMEE MUKHTAR🎁

SADAUKARWA ga Mom manal
Nafisa

Fulanin tashi 😂
Ummu taufeeq
Amrath Amrath
First lady ko nace last lady🤣
Ummu nawaz

Allah yabar k'auna mutane na👍🏻🤗.

🅿6

Bayan an gama d'aurin Auranne aka shiga gaggaisawa da mutane yayinda ake raba manyan bags wanda ke d'auke da manyan goro biskit sweet leman kwali da kuma shaddodi acikin kowa jaka.

Kowa murna yake da hakane suka nemi cewa zasu shiga gidan domin a gaisa da iyayen Amarya """ ai Mlm hadi da gudu sauri sauri yana washe baki yace ah bismillah bisimillah ai gidan kune nan ranka ya dad'e baya ya dawo ya tsaya yayinda yakewa Alhj Sa'id da mutanen sa nuni dasu wuce kan gaba.

Mutane da yawa sungano tsagoron son k'ud'insa da kwad'ayi ne yasa shima bada yarinyar ga babban mutun irin Alhaj Sa'id.

Murmushi Alhaj Sa'id yayi yafar wucewa yayinda sauran ke take masa baya.

Cikin gidan kuwa se gud'a  ake ana Zarah tayi goshin da ba kowace mace ce keyiba seme sa'a a rayuwa.

K'amshin turare ne me kamshin gaske yaja hankalinsu wanda sukai duba ga hnayr da k'amshin ke fitowa se sukaga Ashe Angone da mutanensa.

Nan naga ikon Allah ai gaba d'ayan matan dake gun k'asa naga sun durk'usa kamar masu neman gafara suna gaida vise president.

Laraice kan gaba wajen iya durk'usa se godiya takewa masa yayin da  shi kuma ya durk'usa cikin girma yana gaidata da sauran Abokan nasa.

Cikin rawar murya Larai take amsawa mlm hadi kuwa baki yak'i rufo.

Alhaj Sa'id duba yake ga kowane kusurwar gidan soyake yaga Zarah amma yanajin kunyar tambaya.

Baba maryan ce ta lura da hakan tai saurin cewa bari akira amaryar da kawayenta.

Cikin sauri suka mik'e da Larai suka nufi d'akin dasu Zarah ke ciki.

Kanta a dafe suka sameta amma make up da Aysha sukai mata yana nan sede idonta da yai ja Alamun harta gaji da kukan datakeyi.

Larai ce tafara shiga nan ta iske su sunata kwalliya da fesa turaruka Larai da baba maryam suka wash baki Larai tace yauwa ku d'ad'a gyagygyarawa ga k'usosgin gobnati cen A farfajiya ko kuma Allah yaci daku kuyi mana kamun babban kifi.

Gaba d'aya 'yan matan sukasa dariya Aysha ko fara ah babu a fuskarta bare zarah dako d'ago kai batai ba .

Larai tace maza ku tashi muje kema harda ke ga angon cen nason ganinki.

Zarah mutsi mutsu kawai take da bakinta ita haka take aduk sanda abu be mata dadi ba setai ta mismis da baki wanda ita kanta batasan dalili ba .

Larai ce ta k'ara fesheta da tirare gamida kara mata wata powder a face dinta nan ko tai wani kyau dam cen din ita me kyance.

Hannu ta kamata suka fito da sauran yan matan harda aysha.

Tin daga nesa ya kafe da ido ko k'iftawa ba yayi Yayinda fiskarsa d'auke da Murmushi """" Ministern K'udi'i na lura dashi dan hk da sauri ya d'an zungureshi nan ya dawo dg duniyar tinanin daya shiga .

Itako ko d'aga kai bataiba don batason kallonsa bare jin muryarsa.Abokan sa kam sosai suka yaba kyan zarah gata yarinya me jini ajika lalle abokinsu yayi sa'a.

Nan 'yam matan suka shiga gaidasu cikin kwarwasa suna amsawa aysha ma hk """"  Alhaj Sa'id magana yaiwa da d'aya dg cikin escort dinsa nan aka shiga bawa matan dk gun kud'i ko wacce 30k a cikin ambulan.

Murna kam ba amagana nan suka tashi suka fita matan se godiya suke  """"  Alhaj  sa id mutunne me kunya sosai shiyasa ma yakasaiw zarah magana kwata kwata.

Zarah kam tazo iya wuya jin kirarin da matan ke masa shida mutanen sa  wanda dagaji kasan idon su yarufe akan kud'i suke yin hakan.

Da sauri ta koma d'aki alokacin wani lesa ne a jikinta ruwan zuma anwa d'inkin karamar riga me dan banzar tsadar gaske.

Kuka kawai take.

Larai kuwa tura 'yam matan take akan suje suyi musu rakiya har wajen shiga mota k Allah yasa wani daga cikinsu yace yanaso.

Aiko da sauri suka fita suna yauk'i baran hafsat dake dama akwaita da felek'e

Wayar aysha na hannun hafsat yayinda aysha tini dama tabi zarah d'aki sukad'ai suke damuwarsu dake dama abokin kuka ba 'a 6oye masa mutuwa.

Aysha tace hakuri zaki zarah an riga da 'an daura sede miyi hakuri " d'an kwalin kanta zarah tacire ta had'a hannayent biyu akan fuskarta tana kuka.

Aysha tace zakisani kuka nima dan Allah kiyi shiru nan aysha ta fara kuka haka suka had'u sunayi tare zarah najin kukan aysha da sauri tace na dena amiyat daga yu na dena kuka shine zeyi kukada harya sake ya aureni.

Aysha ta d'ago kanta tace a a karki masa haka wallahi daganin mutumin nan kamili ne kuma yanason ki sona gaskiya bangano alamar wasa a fuskarsa ba.

Uhmm zarah tace kawai nikon ina wayarki ne inji zarah ?  Aysha tace af tanagun hafsat d'an tsaki zarah tayi tace wlh ki kar6o abarki  tin wuri bakisan halinta bane tana iya cewa bata gantaba kuma kinga dole ki hkr in kinajin hankama meda d'an wani naka to hafsat ce.

Dariya aysha tayi tace ki kyaleta zata dawone ai sunfita raka bak'i ne.

Mtsss tsaki zarah tayi tace nide wallahi kije ki anso abarki.

To aysha tace tana murmushi ta share fuskarta ta dad'a gyarata dan kar aga alamun tayi kuka.

Zarah tace kinyi kyau sosai "" aysha tai murmushi tace du kyauna ai kinfini had'uwa.

Uhmm kawai zarah tace"" aysha ta fita waje .

A waje ta iske su hafsat da wasu samari da aka zô dasu wajen daurin auran .

Cikin sanyin jiki ta k'arasa wajen kafa funta har rawa suke dan bata saba keta maza ta wuce ba.

NASEER wanda tinda aysha ta fito idonsa ke kanta ko kiftawa ba yayi sosai tatafi da imaninsa kallonta kawai yake duba ga yanda take d'arare jikinta hakan ya nuna masa tarbiyarta .

Sanya yake da wata arniyar shadda shima fara komai nasa farine Naseer chocolate ne yana da kyau sosai d'ane ga ministern ilimi wanda yake karatu a paris saura rabin shekara kada'ai yagama yarone sosai wanda baze wuce 24 yrs ba.

Le6ensa ya d'an shafa ya tunkari inda aysha keyi.

Tana zuwa tace hafsat dan Allah aramin wayar zanyi kirane .

Hafsat taji dadin maganar datayi saboda batace tabata wayarta ba dan kar agane ba tata bace.

Mik'a mata tai kawai aysha ta shige ciki jitai kawai ansha gabanta yayinda wani kamshi ya ziyarci ruhinta "" tana d'agowa sukai ido 4 seda gabanta ya fad'i saboda bata ta6a ganin saurayi me kyu kamar saba.

Yace ki hkr fa nabaki tsoro ko ?     Batace komai ba kuma har yanzu bata bar kallonsa ba .

Yace abu daya zakimin dan Allah number ki kawai nakeso ita kad'ai ma ta isheni ko zan samu?

Kai ta sunkuyar k'asa tarasa mezatayi ma jitai yana lura da ita sosai yaji dadin hakan dama mace me kunya da tarbiyya yk nema" kawai jitai ya d'ago face dinta suna hada ido ya kad'a mata ido gamida d'aga mata gira yace zan samuko?

Wani iri taji ajikinta da sauri ta hau karanto masa number yana kallonta yn smile yace wayarsa yaciro me tsadar gaske yace ok kara maimaitawa banjiba .

Yana sane yai mata hakan ita ko cikin tsoro ta karanti masa tai ciki da gudu """ dariya yayi ya shafi sajensa yafita waje.

Da gudu ta shigo d'akin da zarah take wacce bacci ya d'auketa .

Mai da numfashi kawai take aranta tana cewa dama 'ya'yan masu kud'i basuda kunya .

Tini suka d'auki hanyar komawa gida zuwa airport dan hawa jirgi Naseer na manne jikin dad d'insa se fara a yake dan shi yau yaga matar aure.

Minister yace yade son naga kana cikin farin ciki"" eh dad idan munje gida zangaya maka "" dad yai murmushi irin nasu na manya ya shafi kansa yace ok.

Kulloli aka shiga shigowa dasu masu yawan gaske wanda Larai ta bada order nan aka hau raba abinci hrdasu kaji soyaiyu.

Musayyit na zaune bayan mota yasa earpiece idonsa rufe yanajin k'ira' ar Al k'ur'ani me girma zuciyarsa na masa dad'i""" jiyai kawai ana ta6ashi ance yalla6ai ai mun iso .

idonsa ya bud'e yana k'arewa gu  kallo da sauri security's suka bud'e k'ofa suna sara masa yana d'aga masa hannu.

Koda aka bud'e gate sea sukai minti 25mnts kafin su iso cikin gidan .

Kafa funsa ya zuro yana shakar iskar gidan wacce take kad'awa sassanya ya lumshe ido .

Bag d'insa na hannun d'aya daga cikin wanda suka kawoshi ma aikatan jirgin nan ya nufi ciki suka bishi da sauri.

Seda suka wace palour 5 sannan ya amshi jakar ya k'ara musu kud'i suka fita suna godiya .

Kamar dag sama momy ta hangoshi itada sauran mutane ai da sauri ta taso shima saurin yake dukkan ninsu suna fara a suna zuwa ta rike masa hannu tana dariya tace saukar kenan ba ko waya?

Murmushi yake yace dama kawai surprise zammiki  da ftn nasameku Ify?

Ah Ify lau Musayyit yaron mama dake haka take fad'a masa lokacin yana yaro "" dariya yayi suka wuce ciki sauran matan kuwa yabisu yana gaidasu ciki kuwa harda k'anwar ummansa.

Kai tsaye bangarensa yanufa da sauri domin so yake yaje yai wanka .

Tini masu aiki suka shiga kawi masa kayan abinci kala kala suna jerewa adining din dake bangarensa.

Toilet ya shiga ya fara wanka abinsa.

Wata 'yar yarinyace keta rigima kan cewa ita lalle sa anfita shopping yanzu momy kuwa se lalla6ata take tana cewa zasu fita anjima itako babyn takiyin shiru.

Momy ce tace yi shiru yanzu yaya Musayyit ya dawo idan yaci abinci seku fita tare ko?

Da sauri yarinyar ta dena kukan tace da gaske momy?   Momy tace eh da gaske mana .

Ai da gudu babyn ta tashi naga ta nufi wani d'aki tana knocking"""

Tsaki wacce ke d'akin tayi tace wane zedameni a halin yanzu aikin banza kawai.

Jitai ana cewa anty anty ki bud'e ya Musayyit ne ya dawo  """  ai da gudu ta tashi jikinta ko sitturar kirki babu ta bud'e kofa .

D'auan babyn tayi ta d'agata sama tace da gaske kike ya Musayyit ya dawo ?   Yarinyar cikingwaranci tace eh ya dawo inji momy.

Hijab kawai naga ta zura kota kan babyn bata biba tai hanyar waje.

Wanka yake cikin nutsuwa bayan ya gama tawul kawai y d'aura iya k'ugunsa zuwa k'wairinsa ya fito .

Ganin mace kawai yayi bisa gadonsa zaune "" .

Zarah zarah kitashk bacci ya isa gaka kisake sabon wanka yanzu babanki yace a shiryaki yanzu za a tafi kaiki """ ko bakajina zarah na jinta domin kuwa ta jima da tashi dg baccin wani ihu zarah tasa se kace wacce akaiwa mutuwa.

Dan Allah ammi kiyi hakuri karku kaini wani gari bansan kowaba banida kowa acen dan Allah ammi kuyi hakuri.

Larai tace iyyye ai Alhaj Sa'  id shine uwarki shine ubanki maza tashi  tinda dama ba wata gayyar qawaye kikai ba .

Haka zarah ta shiga toilet tana wanka tana kuka.

cikin awa d'aya aka gama shiryawa malam hadi kuwa shine kan gaba wajen riko hannun zarah ya kaita d'akinsa yakamayi mata nasiha kan cewa tabi mijinta idan ta sake ya kawo kararta tai masa wani abu seya sa6a mata.

Mutane dayawa aka tafi dasu wanda jirgine dama Alhaj Sa'id yabada kud'i akaisu daga kano zuwa abuja.

Larai ma tai mata natafadan me harshen damo.

Nan suka kama hanya se airport

Kallonta yake da mamaki yace wayaki ikon shigomin d'aki?   Ko kuwa kinzo kinuna min karuwancin nakine?

Fa 'ezah tace haba ya Nusayyit dan kai nazo bikin nan badan kowa ba saboda nasan dole zaka dawo a lokacin nan yakamata ka tausayamin ka dubi irin son da nake maka .

Tsaki yayi fuska a had'e yazo daf da ita mikewa tsaye tayi ta kama hannunsa tana kuka """" wani mari ya d'uketa dashi wanda sedataga taurari na yawo .

Cikin daga murya  Yace maza kibarmjn d'aki banza wacce batasan darajr kantaba get out  na fada miki banasonki ki fita a rayuwata.

da gudu ta fita waje dafe da kuncinta tana kuka .

.ummee ce taku 🤗🤗😘👄
[31/08, 16:19] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBAN*
*MUTUN*

Creating and written  by

UMMEE  MUKHTAR 🎁

SADUKARWA GA UMMY ONTOP   Naga an fara sabon novel  'yar ta Adda da ftn bazatayo kaina ba🤣🤣😂😂😂   Allah ya k'ara basirah.

🅿7

Musayyit  Fa'eza na fita yai tsaki yabi k'ofar da kallo yace this gal was fallen in love with me """"but I don't love her""" why not daba zataso wanda suke sontaba se shi ?

Wani tsaki ya kumayi ya shiga gyara jikinsa seda ya gama k'ak'ale k'ak'alensa sannan yasa k'ananun kaya yabi wat kwana ida zata sada shi da dining area.

A filin jirgi kuwa security na tsaitsaye kamar sojoji  da alamu zuwan Amarya kawai suke .

K'arfe 5.30 dede sk sauka 'yan kawo amarya se baza ido ake """""" cikin girmamawa securities d'in ke gaida manyan matan dake rik'e da hannun Zarah.

Zarah kam kuka harta gaji yanzu ajiyar zuciya kawai tk.

Motoci suka shiga wanda aka tanadar musu suka d'auki hanya.

Aysha na daga gefe se kallon zarah tk tana tausaya mata gashi amma ta auran da bataso gashi an kawo ta inda batasan kowaba.

Kiran wayarta ne ya shigo wanda ko bata saniba tasan mayen saurayin nan ne na d'azu  dan ba wanda yk da number ta se zarah."""" da sauri t kashe wayar ta jefa a jaka.

Fa 'eza na shiga d'aki tai cilli da hijab  wanda se atime d'in naga ashe dg ita se brazia se skin tye.

Kuka ta kamayi sosai tana cewa ya musayyit menai mk menai mk baka sona ?  Ko banda abunda kk sone ajikin mace?

Tsam ta mik'e ta share hawayenta ta fuskanci tafkeken mirror d'in dk manne a d'akin tana k'arewa kanta kallo.

Wani murmushi tayi tace dani kake yi senayi maganain ka da maganin taurin kanka sena sauke mk duk wani gigi dk kanka inde nice fa'eza.

Zarah kanta a sunkuye jitai kawai ana cewa a fito nan ta d'ago kanta dan kallon inda Allah ya kawota .

Gabanta ne yai mummunan fad'uwa sanda tai arba da tafkeken gidan wanda ko a mafarki bata ta6a zatoba sede kawai ta gani a fina finan k'asar waje.

Sukansu 'yan kawo amaryar cike sk da mamaki .

Nan baba maryam ta riko hannun ta wanda keta karkarwa tin d'azu.

Fad'ar tsaruwar gidan 6ata lokacine komai yayi a kwai masu gadi har su 5   se securities  da sojoji wanda aka zube musamman domin kula da gidan da abinda ke cikinsa bare ga amarya ta zo.

Haka suka shiga se rab ido  suke rasa inda zasu zauna sukai domin kuwa se wuce palour suke birjik adon kowane palour dabanne .

D'akuna kam ba a magana duk inda suka lek'a se suga komai a kwai   .

Baba maryam ce tace a kira mata d'aya dg cikin wanda suka rakosu .

Da sauri yazo gunta cikin ladabi  yace gani """"  in ina takamayi secen tace dama tamvaya zanyi dan Allah inane bangaren amaryar munga komai da yawa ne to munsan yafi karfin zaman mutun d'aya shine nk tambaya wane wajenne nata ita amaryar?

D'an murmushi yayi yace ai hajiya nan gidan tane ita kad'ai ira uwargidan ba unguwama d'aya suke ba.

Baki Baba maryam ta bud'e Aysha dk gefe ido ta zare a ranta tace wallahi nasan yanda zarah tk da tsoro bazata yarda ta dinga kwana ita d'ayaba.

Baba maryam tace to to ngd ko yauwa ngd """ gaba d'aya ta daburce yayinda kowa ya shiga yawo acikin gidan kamar wanda suka shiga wani k'aramin city😂.

Wani d'aki a ka kai zarah  wanda duk abinda suke bata ko d'ago kaiba domin wani haushi da 6acin raine suke ziyartar zuciyarta.

Ah zarah wallhi kinyi sa'a acikin mata ai se k'alilan kai masha Allah   wallahi kamar abarni anan "" hk sukaita santi   zarah kuwa idontama ya bushe hawayen yak'i zuwa.

Nan suka baje suka rasa inda zasu zauna dg wancen sashin se wancen .

Nan suka bar zarah   ita kadai .

Aysha ce ta shigo tacewa baba maryam ga wasu maza cen a waje  sunce kizo

Da sauri ta mik'e ta fita """ tana fita ta gansu dauke da kuloli na abinci har 15 se wasu kulolin guda 8.

Baki ta bude tace sannunku wannan fa ?   Ah dama yalla6ai ne yace akawo muku sbd nan zaku kwana idan yaso gobe se amai daku gida  ga wannan abincine    idan be I saba sekuyi magana """  dg hk suka juya sukace mata se anjima.

Baki ta bud'e tace yau naga ikon Allah  yoni daza abarni agidan nn wlh zama zanyi.

Nan ta kira sauran aka shiga diba ana shiga dasu gidan .

Kowa ce kula idan aka bud'e abinda ke cikinta daban ne

Kaji soyaiyu da farfesu se nama soyaiye da farfesunsa .

Soye soye ga sunan kala kala cake meat pei sncks kala kala fride rice har wani abun ma basu san shiba.

Kitchen  sukaje wanda gashinan gari guda ne me girman gase spoon suka diba da plate suka dawo palour

...ciki aka ware aka shiga aika masa da sak'o

Baba maryam naga ta dauki wani plate ta nufi d'akin da zarah tk wanda tin dazun da suka barta suka kama yawo cikin gidan.

Kwance ta ganta dafe kai idonta yai ja tace suba hannallahi zarah Ify?

Umma kaina ke ciwo uhmmm zaki ware ne gajiyar hanya ce .

Ai hkr wlh d'azu nayi typing me yawa ya goge amma gobe insha Allah zakuga me yawan gaske🤗🤗🤗🤗😘😘😘😘😘😘

[31/08, 16:19] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBAN*
*MUTUM*

Creating  and Written
By

*UMMEE* *MUKHTAR🎁*

This page is ur MOM MANAL .Sarkin rigima😂. Allah yabaki Ify ya qaro sauki ..

🅿8

Nasan gajiyar hanyace tashi ki daure kici """ zarah bataso tai mt gaddama dan hk ta mik'ea hankali ta tura mt plate d'in tafaraci kadan kadan.

Minti 2 tace ta k'oshi.

K'yaleta tayi don itama bataso ta takura mata a wannan lokacin.

Bayan sungama ne sukaji shigowar motoci gidan da sauri 'yam matan suka lek'a don ganin su waye """maza suka gani ko wanne sanye cikin kwat da glass komai bak'i ne ajikinsu har shoes dinsu """" wani ne ya fara shigowa yaiwa sauran matan magana cewa anzo d'aukan sune za a wajen dinner .

Manyan matan sukace ah to kuramu gamunan zuwa .

D'akin da zarah tk suka shiga suka shedawa baba maryam cewa anzo daukan sune.

Baki tq washe tace lalle kaji inda ake abu aiko yanzu wlh zamu tashi Aysah ce ta kallesu da mamaki donko ko sallah ba suyiba amma suke shirin tafiya. Aysha ce ta ciro wayar zarah ta kunnata ta mik'a mata tace gashi da badan na tuna na dakkoba da shikenan sede ase wata """ jiki a sanyaye zarah ta amsa fuskarta taija sosai harta d'an kumbura sbd kuka.

Baba maryam tace yauwa aysha ku zauna tare da ita muzamuje mudawo dan ba abarta ota kadaiba .. to kawai aysha tace dan itama batason zuwa.

Nan da nan aka shirya se murna suke suka motocin suka bar gidan .

Ya rage daga aysha se zarah.

Kuka zarah ta 6arke dashi tai cilli da mayafin kanta ta had'a kai da drower .

Aysha ta dafata tana lallashinta haba zarah meze dameki  kin bude ido kina gidan ki kuwa?

Dazu dana zaga baya har wani swimming pool nagani me adon heart   komai yayi ki kwantar da hankalinki ga gidanki kamar mutun ishirin ne zasu zauna kuma duk ke d'aya .

Dago kai tayi tace ni duk wannan be dameni ba wlh kawai ninasan menakeji.

To wani waje na musamman aka kaisu su hajara dasu baba maryam se washe baki ake nan suka tadda mutane mata da maza zazzaune ba wasu masu yawa bane nan suma aka basu wajen zama  da aka tanada dominsu.

Daga gefe Alhaj sa'id ne da uwargidansa   sun sha kyau sosai se d'aya bangaren  yan uwane da abokai   se baby shukrah dake kusa da fa'eza  """  fa 'eza kam se raba ido tak ko zata musayyit amma ko k'eyarsa bt ganiba abunda ya harzukata kenan.

Alhaj  sa'ed yaga 'yan uwan zarah amma se raba ido yk yaga koze ganta amma bata agun.

Waya yaiwa d'aya dg ciknin yaransa cewa ina amaryar?

Cewa yai wlh besani ba  amma bari ya tambayi  daya dg cikin iyayenta mata.

Nan yaiwa inna hajara maganar cewar ina amarya   baba maryam najin hk tai salati tace mun barta gida ai mun dauka ita ba inda zata ne oh ni 'yan nan .

Alhaj sa id ya gayawa yanda akai cewa tn gida an barta.

Ransa ne ya 6aci sosai har momy ta kula dashi wacce tasha wani arnen less na manyan mata.

Musayyit na kwance a tafkeken gadonsa yaji wayar Dadynsa da sauri ya d'auka yace dady barka da dare.

Yauwa kawai yace kana ina ne ?

Um um dama nima ina kan hanyata ta zuwa gun dinner """ hmmm dady yace dan yasan k'arya yake donshi bayason shiga mutane sosai.

Yace ok kaje cen gidan dana ta6a watan nin baya wanda aka ginashi d'in nan kaje zaka d'akko amaryata yanzu muna jiranka dg hk ya kashe wayar.

Musayyit na cire wayar dg kunnensa yace oh no banson fita wlh amma ba yanda zanyi.

Hk ya shirya cikin wani yadi me walwali light coffee ne shoes ma hk se hula da agogo duk iri daya.

Wanka yai da turare  yasa chewgum  abikinsa me kamshi ya nufi gidan zarah.

A gun dinner tini an fara raba kaye kaye na gani  ma fada dama na ciyr ciye.

Alhaj    sa id idonsa na kan hanya ganin zarah.

Masu gadi suna ganin motar Musayyit da gudu suka bude suna daga masa hannu.

Koda yai parking ya fito gidan ya qarewa kallo lokaci daya kuma  yasaki wani murmushi me tsada ya fara taku.

Aysha ce ke rik'e zarah wacce tk k'ok'arin fita ita alallai seta gudu dg gidan mayafine kawai a hannunta da gudu ta fito aysha na binta abaya  tana shan kwana Musayyit ya kawo kai sukai karo ta fad'o jikinsa """"  da sauri ya rik'eta kanta lille6e da mayafi dan hk be samu ganin fuskar kowaceba """" jikinsa rawa kawai yk dan be ta6a had'a jiki da wata mace ba"" da sauri  ta juya masa baya itama se kyarma take yayinda  takejin  gabanta  na fad'uwa   """"  Tak'i gab tak'i baya hk shima hk sekace wanda aka kafe agun kallon baynta kawai yk  numfa shinsa na fita da sauri   Bata juyo bayanta ba tafara magana cikin kuka kūka tace dalla malam bk gani zk bige mutane ?

Sosai  yaji haushi dan ba a ta6a yimasa hk ba  dakewa yai yace ni kk cewa dalla?

Eh na fad'a d'in zarah tace tana k'ara rufe fuskarta.

Da gudu aysha ta k'araso wacce tk haki  ta fisgi zarah wacce jikinta ke rawa ita azatont ta dauka Alhaj  sa id ne a shigo.

Aysha tace muje ba inda zaki ya daga zuwanki gidan miji kice  ke gida zaki .

Musayyit ya sauke ajiyar zuciya   wanda se a lokacin  aysha taga  mutun agun.

Sosai kyansa ya birgeta   gaskiya guy yayi ba k'arya   ."""""   Sannunko  abinda   yacewa aysha kenan  cikin rawar murya tace yauwa """"  hannunsa ya zuba a aljihu yace wannan itace Amaryar?

Zarah jitai kamar ta ta6ajin muryar  kamar ta juyo se kuma ta fasa.

Yace ok amma meyasa takeson zuwa gida ?

Ya salam zarah ta fad'a cikin zuciyarta   wannan muryar da alamu mutun d'aya keda ita a duk duniya sosai voice dinsa yk shiga kanta harta na rufe ido.

Aysha tace ah ah dama kawai de ummanta takeson  gani.

Wani murmushi yayi yn k'arewa zarag kallo ta baya wanda bayanta kawai yk gani """ cikin murya sassanya yace duk wata mace tana murna da wannan ranar inde har tanason mijin data aura amma yanzu na gane wani abu d'aya dan hk kuje ku kwanta kawai seda safe  dg ya juya yai waje kamshin turarensa yadaki hancin zarah.

Da sauri ta juyo bayansa kawai tagani idonta taf kwallah   a ranta tace duk da ban ganshi ba Allah yayi halitta anan tace aysha dubi bayansa  tsayaiyen namiji matashi  dashi kisan cewa an cuceni.

Kul karki k'ara babu kyau matar aure ta dinga yabon wani namijin daba nataba.

Muje kawai .

Musayyit  da sauri ya koma mota ya zauna ya kasa tada ita ya d'aga kansa sama yana tina karon da sukai da waccen yarinyar d'azu.

Tsaki ya d'anyi yace dady ma ya rasa wacce ze aura se wacce batafi 17 yrs ba gaskiya ya cuci momy wlh  kuma yarasa wacce ze auro se mara kunya tana gani karo sukai amma ta d'ora masa lefi   .

Wayarsa ya ciro  ya kira dad yafada masa cewa bacci tk   ""  dad yace bakomai ya kyaleta.

Se waje 11:30  aka watse aka dawo dasu gida ko wacce ta za6i inda zata kwanta cikin katifu da gado masu laushi  .

Wanda da safe ne zasu daukin hanyar gida.

A subar fari sukai sallah aka kawo musu abun kari   aka fita sauran kulolin jiya wacce ko rabin abkncin basu ciba sbd sunad yawa kulolin zarah ma tai wanka sanye tk da dogwar riga fara me duwatsu fuskarta tai fayau ba kwalliya a face d'inta.

Tana d'aki suna hira da aysha .

Alhaj s'id ne ya shigo cikin shadda ruwan zuma me kyau tayi masa kyau abunka da farin mutun kuma kyakykyawa.

Gaisawa sukai cikin girma yayinda ya bawa kowa takarda wacce kud'ine a ciki   yace idan sun

shirya mota na jiransu.

Nan ya fita suna ta mai godiya ""kai zarah kinyi dace ga kudi a miji me kyau sede kawai ace yayi sa an babanta.

Yomeye aciki   wallahi babu komai hk sukai ta  hira suka lek'a sukace ayha ta fito za a tafi da kuka suka rabu zarah se ihu take baba maryan na turata ciki.

Da hk suka bar gidan suka barta tana kuka.    Da gudu ta koma d'aki ta saki kuka ta kwanta tana birgima tanacilli da duk wasu kayan glass dk wajen.

Ummulo 😘😘😘😘
[31/08, 16:19] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBAN*
.          *MUTUN*

Creating  and wretten by *UMMEE* *MUKHTAR*🎁

🅿️9

Seda  Zarah tai me isarta sannan ta koma kan bed ta kwanta idonta rufe se sauke ajiyar zuciya tk.

Tini ma'aikatan dk gidan mata ne zasukai su 3 suka shiga gyara gidan cikin lokaci kad'an suka gama """"  wata me aiki ce ta shiga wani d'aki wanda ba komai ne acikiba se turarukan wuta kala kala da Airfreshner  masu d'an banzan k'amshi wanda cike sk ad'akin kamar zasuyi magana.

Nan da nan ta shiga turare gidan ko wane waje seda taiwa turare kuma ta fesa na fesawa.

Tini gidanya dau kamshi me dad'i.

Zarah dake kan bed kawai ta dinga jiyo kamshi tashi tayi ta goge hawayenta tafara taku cikin sand'a"""" d'an lek'owa tayi sede bataga kowaba amma ga gurinan a gyare se zuba kamshi yk""""..

Kallon ko ina take dan hk ta fara tafiya tana bud'e duk wasu d'akuna dk gidan ""hakama tabi kowane palour da kallo gasunan da yawa birjik sosai gidan ya bata sha'awa dan bata ta6a tinanin zata zauna a gida irin wannan ba .

Cikin muryar kuka tace ha gida har gida amma bada saurayi zanyi rayuwa ba wannan abun da ciwo""""inama da matashin namiji zanyi rayuwa agidan nan danayi farin ciki sosai.

D'akin ta koma ta kwanta se kuma ta kamajin sanyi har tana karkarwa .

Gidan Alhaj Sa"id ma kowa ya tafi se fà'eza wacce tacewa momy ita fa tazo kenan bazata komaba """ momy dad'ai taji dama batada wata budurwar 'ya agabanta in band khairat .

Musayyita ne ya shigo gidan kai tsaye bangarensa ya nufa """ yana shiga yaga fa'eza se goge masa kaya take "" da mamaki ya tsayayn Kallon ta wanda ita sam batasan ya shigo ba.

Hannunsa ya zuba a aljihu kawai yana kallonta.

Jitai am buga mata wara uwar tsawa wacce tasa seda ta firgita tai hanyar toilet:":"

Gidan ubanwa zaki a toilet maza zoki fice tinkafin ranki ya 6aci"""" se yanzu taga ashe shine dan hk ta saki fuskarta gamida dafe k'irji tace wlh ya musaiyyet ka tsoratani na firgita.

Eh nine wayace kita6amin kaya? Wama yace mk kayana ba a goge sukeba?

Taku tayi har gabansa tana murmushi shiko idonsa akanta cikin d'aurewar fuska ""a haka tazo

har gabansa tsugunawa tayi gamida rik'e kunne tace kai hkr bazan sakeba.

Kallonta kawai yk yace ok tashi kije na nagode ko amma nex time karki kara karan banin ta6a kayana kinjiko.

Komai nasa burgeta yake ciki kuwa har fad'an dayake mata domin tindaya fara mouth d'insa kawai tk kallo.

Yace jeki inason zan wankane""" jiki ba k'wari ta mik'e yabita da kallo.

Tsaki yayi yace narasa yadda zanyi da yarinyar nan amma bari dad ya dawo wlh seta koma gidansu.

Karfe uku dede me aiki se buga d'akin zarah take amma taji shiru "' a k'alla takai minti shabiyar tana knocking amma ba a budeba.

Zarah kuwa najinta kawai zazza6ine ajikinta ga yunwa tanaji ahaka ta taso dakyar ta bud'e kofar"""" tana budewa sukai ido hud'u da Merry sanye cikin kayan aiki wanda akai dominsu masu aikin.

Zarah tace Ify ? Cikin ban garma merry tace dama na shirya miki lunch ne tin d'azu shiyasa nace ari na sanar dake.

To kawai zarah tace ta koma d'aki.

Tana shiga toilet ta shiga don yinwanka kallo ta tsaya yi ganin haduwar toilet d'in sosai ya burgeta komai yayi ga kuma kayan kamshin toilet nan da yawa gamida sabulai masu kamshi da mayukan wanke kai .

Seda tai wanka sannan ta fito always ta d'akko wanda dama tin kafin su taho ta fara period.

Doguwar riga ta atamfa tasanya dikin ya matseta sosai gashinta ta gyara tai simple makeup.

Turare ta fesa sannan ta fito dan cin abinci.

Flask ne dayawa gasuna jere taci duk abunda take so .

Farfesune na kifi dana kaza  se white rice da stew d'in cabbage wanda yasha nama aciki'   Se juice na kwali da kuma wanda aka hada agidan '"  se potatoes soyaiye da kuma wainar kwai.

K'ugu zarah ta rik'e tana kad'a kai tace eh ga mayunwaciya ba ai dole yasa akawo min wannan cimar sbd game cikin zani '''"   Amma mutumin nan d'an rainin wayone wlh.

Zama tayi ta zuba kadan a plate tafaraci.

Tini  'yan kawo amarya suka je gida yayinda aka basu kud'i da turamen atamfofi.

Sosai Lari taji dad'i  yayinda suke gaya mata kyan gidan zarah.

Karfe  7 dede iyalan sun hallara a babban palour  wanda Alhaj   Sa'id ne se momy fa 'eza da khairat se Musayyet.

Alhaj yai gyaran murya yace musayyet yabatun aikin nan ince komai ka kammala?   Musayyet yace eh dad angama komai shiyasa ma na taho  'yace gud  kallon fa'eza yai yace amma de anan zaki zauna ko kinga momyn ki taji dad'i.

Cikin jin dad'i  tace eh dama nazo kenan saboda nagama karatu aiki kawai nk jira "" dad yace masha Allah  seki bawa Musayyet takardun naki  kinga seki aiki a d'aya dg cikin compayn mu ko?

Cikin jin dad'i tace ngd dady Allah yaja kwana.

Nusayyet ko jiyai kamar an watsa masa ruwan zafi se harara yake aika mata dasu itako ta gefen ido tk kallonsa tana murmushi da wannan damar ne zata samu auran misayyet.

Sosai ya had'e rai yace dad datayi zamanta agidansu acen ma ai seta dinga tafiya aikin ko?

Alhaj Sa'id yai murmushi irin nasu na manya yace a a tai zamanta nan gidan nima zanji dad'i koba komai ai kun k'aru kunzama ku 3 a gidan '" danguntun tsaki Musayyet yayi wanda shikad'ai yaji abunsa nan take ya tashi yace yanason zuwa wani gunne.

Mony kallonsa kawai take domin ta gano bayason zaman fa'eza a gidan "" murmushi kawai tayi tace Alhaj yakamat fa katafi kabar 'yar mutane a gida tin jiya ita d'aya tinda kowa ya tafi ai sekaje Allah ya tashemu Ify.

Da sauri khairat tace dad nima zani?

Kumatinta ya shafa yace to shikenan semu tafi tare amma yanzu zani unguwa na dawo semu tafi yareko?

Kai kawai ta d'aga masa nan ta kama tsalle da murna .

Tashi yayi yace to madam seda safe """ kallonsa tai tace mukwana Ify.

Fita yayi nan securities da escort d'insa suka rufa masa baya.

Momy murmushi tayi tace namiji kenan .""""  Fa'eza tace momy naji kina cewa yabar 'yar mutane kina nufin k'aramar yarinya ya aura?
Momy 'yar dariya tayi me ciwo tace eh fa 'eza yarinyace kimma girmeta a shekaru babu yanda na iya halin namiji sede ka barshi kawai.

Tsaki fa-eza tayi tace wlh harkin samin tsana yarinyar aikin banza.

Momy tace kul karna kuma kumajin hakan .
Dake tasan halin momy bataso ayawaita magana inde ta 6acin raine yasa tai shiru da bakinta.

Musayyet kuwa d'akinsa ya koma ya kanta yanajin haushin abinda dad yace wai fa'eza ta zauna agidansu.

Wayarsa ya ciro yafara kiran layin zarah.

Zaune take a d'aki tayi tagumi idonta hawaye na zuba taji ringing d'in wayarta.

Da sauri ta d'auka sede ba suna "": cikin murya sirirya tace hello wace ?

Murmushi yayi yace nine de na ran nan kintina?

Ta gano muryarsa dan haka tace menene to ko yauma momyn kake nema?

Dariya ta bashi ya gyara kwanciya yace no yau baby nake nema.

D'an murmushi tayi tace malam kai hkr da matar aure kk magana """ be d'auki zancen da mahimmanciba a tinaninsa kawai batason magana dashine.

Yace haba baby ai kya tsaya kiji mena keso dg gareki.

Wasa take da hannunta tace to inajinka yace wlh tinda naji muryarki ran nan naji kin kwantamin a rai dan Allah karkice bakya sona pls.

Jitai maganar ta soketa har cikin zuciyarta se jiyai kawai tana kuka kuma takashe phone d'in.

Sosai hankalinsa ya tashi zubur ya mik'e akan gado yana k'ara kiran layin sede akashe wayar take.

Bango ya kaiwa duka nan take idonsa yaija""' menene matsalar yarinyar nan shikam da yasan inda take da yaje ya lallasheta gashi wayarta a kashe .

Yanajin kukan tane har cikin zuciyarasa.

Kansa ya kifa a kan k'aramin center table ya fara kuka  Allah ya jarrabe shi da son wacce bema ta6a ganintaba wannan wane irin abune gashi ga dukkan alamu a cikin damuwa take.

Zarah cilli tai da wayar ta fara kuka kamar ranta ze fita """"  yau gashi  wani matashi yana furta mata kalmar so Alhali tana gidan aure""  ga dukkan alamu koma wayeshi tabbas shid'in kyakyawane kuma ze iya nunawa mace soyaiya amma an tashi an bata wani babban mutun wanda ta tabbata be iya soyaiyaba kuma koma ya iya ita yai mata girma bazata iya ba """ kuka ta k'ara fashewa dashi me cin rai.

Alhaj  Sa'ed yana zuwa aka bud'e musu gate suna d'aga masa hannu "' seda akaje wajen parking da motaci sannan susuja koma baya shikuma yai musu sallama ya tunķari  gidan   cikin farinciki.

Zarah na kwance tana sana'ar ta ta kuka taji knocking  wanda  ta tabbata megidan ne  da ido ta zaro waje tana k'ara sautin kukanta.

Ummulo ce take   😘
[31/08, 16:19] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBAN*

*MUTUM*

Creating  And  Written  by
*UMMEE*  *MUKTAR*🎁

SADAUKARWA ga  my k'awa
Fateemah Zarah 😍  Allah yabar manake kodan musha chapter😂  Sarkin Comedyn Family And Friends  inayinki irin over d'in nan🤗.

🅿10

Zarah ido ta zaro waje ta saki kuka gamida k'unshe baki tanaja baya seda taje har k'arahen gadon jikinta se rawa yk ''
Knocking ya farayi wajen so hud'u amma yaji shiru kamar bame rai a cikin d'akin """" wani d'an guntun murmushi yayi irin nasu na manya be hkr ba yak'ara knocking amma tsit kakaje ""

Wayarsa yaciro yafara kiran layinta amma wayar na kashe ' Ahankali ya furta tokode yarinyar nan tayi bacci agogon hannun sa yakalla seyaga k'arfe 8:31 kallon k'ofar ya k'arayi yace may be kotayi bacci ne amma yakamata naga lafiyarta """

Duk abinda yake fad'a zarah na jinsa itakam tsoro ne fal ranta gamida fargaba"" cikin sand'a ta bud'e k'ofar toilet ta shige namma ta banko k'ofa tai zaman ta a wani hadaddan bahon wanka karami madedeci kamar dan ita akayi ,...

Haka yaita knocking amma shiru " kai tsaye wani corridor ya nufa wanda ze sadashi da wasu dakuna na musamman """".

Yana zuwa ya cire kayansa ya shiga wanka gami da d'auro Alwala.

Haka yaita sallah yana rok'on Allah akan Allah yabasu zaman lfy ya kore sharrin dk cikinsa ya kuma bashi ikon yi musu adalci.

Bayan ya idar jallabiya yasaka ya hau kan bed ya d'au remote ya kunna A.C ya kwanta sede bacci ya gagareshi domin yaci burin wannan ranar amma yarinyar nan taki bude masa kofa '''
..zaune ya tashi yace kai inagafa bacci tayi ai dole tai bacci da wuri domin kuwa tagaji.

Laptop d'insa ya d'akko ya shiga tura wasu sakonni .

Zarah kuwa jin shirune yasa ta fito da alamun ya tafi """ idonta ta goge takoma toilet tasakw wani wankan ta shafe jikinta da mayuka masu sa fata tai kyau sannan ta zura kayan bacci.. jitai cikinta na k'ugi domin kuwa tanada olcer tana sata saurin jin yunwa """ tin wajen karfe 7 na daren merry ta jera abinci a dining amma zarah bata fitoba.

Zarah cikin murya k'arama tace   wayyo cikina yunwa nakeji """  A hankali ta tashi  nan ko idonta yagane mata wani k'aramin firij dk d'akin da sauri ta nufeshi tana bud'ewa kuwa taga nau in drinks kala kala  harda cake wanda yk acikin kwali sannan kuma k'unshe a cikin leda me ķ'yalli da sauri ta d'ebo ta meyawa da drink tafaraci .

Seda ta k'oshi tai brush sannan ta kwanta barci taja bargo tai addu'a se bacci.

K'arfe 12 na dare Musayyet babu alamun bacci a idonsa  tinani kawai yake ta ina zega yarinyar nan ""?  Hak'ik'a shikam yakamu da soyaiyarta wayarsa ya jawo ya k'ara bugawa amma still a kashe tk d'an tsaki yayi ya kwanta idonsa na kallon saman d'akin ,,,,,  .wayar ya kuma dauka ya kalli number wacce yai mata saving da funny gal.  Wahasp ya shiga aiko nan yaga  itama tana hawa online amma alamu ya nuna kwana biyu bata hauba murmushi yayi kawai me k'aya tarwa """yana shirin aje wayar yaga kiran fa' eza na shigowa""""" da mamaki yabi number da kallo yace wannan kuma ubamme tk nema a wannan lokacin?

Be d'aga ba hk taita kira wajen so 6  yace oh no wannan ya rinya a kwai mayya cikin fad'a yai pickin call  yace what?

Daga ita se wata riga wacce da ita gara babu tace haba ya Musayyet wai dan Allah menai mk ne duk kabi ka tsaneni kamar ba 'yar uwakka ba ?

Numfashi yaja ya gyara kwanciya yace menene to ?

Murmushi tayi ta samu abunda take nema dan hk ta kashe murya tace wlh nakasa baccine ? Kansa ya shafa sannan yace kuma ni meye nawa acikin rashin yin baccinkı?   Kuka tafara tana cewa  Addu'a nakeso  kazo kaimin irin wacce kaimin watannin baya lokacin ina tsorata d'in nan wallahi yanxuma ina rufe ido sena dinga ganin kamar wasu baqaqen mutane sunamin yawo. Cikin ransa ya yarda domin yasan tana da Aljanu  .

Fa 'eza nada Aljanu wanda tasha fama dasu shekarun baya .

Hakan yasa yanzu ya yarda da zancenta """""":
Wani ihu ta k'wallah wanda shikansa seda ya razana da sauri ya aje wayar
cikin azama ya tashi ko riga babu jikinsa .

Sauri yake Sosai ya nufi d'akin fa"eza dan besan a wani hali tk cikiba.

Yama manta daya fad'awa momy hankalinsa duk yayi gaba.

Yana zuwa ya turo k'ofar d'akin aiko yaganta se juyi take akan gado.

Da sauri ya nufe ta tsayawa yai ko ta6ata beba ya farayi mata addu a yana tofa mata """ tashi tayi tafara cilli da kayan d'akin ganin zataiwa kanta rauni yasa ya cukumeta ya riketa sosai ya kwantar da ita akan gado yana kwalawa momy kira .

Momy kam sam batajiba kasan cewar a kwai 'yar tazara tsakanin dakunan su.

Musayyet yarasa yanda zeda ita Addu a yk mata amma kamar tinzurata yake ":"" gaura mata mari yayi aiko ta zuba wani ihu nan yasake karamata wani aiko nan take tace ya Musayyet nifa kake duka.

Dagata yayi daga dannar da yai mata yace sannu ko ai yanxu dasukaji duka sun dawo hankalinsu """ hanyar fita yayi da sauri ta biyoshi ta rungumeshi tace dan Allah ka Aure ni wallahi inasonka ina mk son da bana yiwa kaina.

Da k'arfi ya finciketa yace oh yanzu nagane Ashe Aljanun naki naki na iskancine """toki kiyayi had'uwarmu nan gaba bazakiji da dad'iba daga yai waje tabishi da kallo zuciyarta na mata suya .

Wannan wane irin mutunne me taurin rai da bak'ar zuciya haka.

Amma wallahi bazata k'yaleshi ba su zuba su gani.

D'akinsa ya nufa babu kowa agun momy kuwa a time d'in ta fito wucewarsa kawai tagani gashi ko riga babu jikinsa """

Da sauri ta nufi d'akin fa'eza amma bata bud'e k'ofa ba jitai fa"eza na kuka tana cewa nizakaiwa hk wallahi sena aureka komai abunka.

Da sauri momy tai d'akin taga fa 'eza zaune jikin gado tana kuka ,,,dafata tayi tace lafyanki kuwa ?
Da sauri ta rungume momy tana kuka tace momy shine ya Musayyet ne ..

Cikin damuwa momy tace subahanallahi meyai miki.?

Kuka taka'rayi  tace momy ya Musayyet ne tinda yadawo kullun seyazo dakina nace masa miyi aure yak'i wai akwai wacce yakeso ta k'arashe maganr cikin kuka.

Momy jawota tai dg rungumar datai mata suna fuskantar juna tace da gaske kikeyi?

Cikin kuka tace eh momy    ki tambayeshi nasan baze fad'i gaskiyaba .

Momy kallon gadon tayi wanda yk a ya mutse kuma ta tino da wucewar musayyet data gani dazun ko riga babu jikinsa .

Kai ta dafe tace innalillahi wa inna ilaihi raju'un" wannan wane irin abun kunya kukesi kujawi mana ?

Kanta momy ta dafe wanda ke mata ciwo yanzun gamida runtse ido.

Tayama za ai haa ta faru gashi taga hujjoji da idonta babu damar t k'aryata.
Inda wani ne ya fad'a mata haka zata k'arya ta domin tasan ba halinsa bane shida ko mata basu dame shiba ."" Amma ba a shedar mutun dari bisa d'ari tunda harsuka kad'aice shida ita to shed'anne na ukunnsu.
Ta k'ara dafe kai tace ya ilahi.

Musayyet nashiga d'akinsa yace zanyi maǵanin yarinyar nan wato ni zataiwa iskanciko?

Kai ya dafe  take gabansa ya fad'i jin irin  bugun da momy take kuma tana  k'wala masa kira cikin d'aga murya  a wannan daren.

Love you All my fans🤗😘
[31/08, 16:19] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBAN*

*MUTUM*

Creating And Written by

UMMEE MUKHTAR🎁

This page is urs

Nafeesa
Mom fauzah
Maman umar
Maryam usman.

Nagode sosai Allah yabar k'aunah❤.

🅿11

K'ofar yabi da kallo wacce momy ke bugata kamar zata 6alla"" cikin rawar jiki ya nufi k'ofar yasa hanu ya bud'eta"""  yana bud'ewa momy ta hankad'o masa fa'ezah har tana cin karo da kafad'arsa kamar zata fad'i yana kallonta ko k'ok'arin  rik'eta beba dan mugun haushinta yakeji yanzu.

Momy idonta taf da hawaye  take kallon jikinsa daga k'asa har sama """ shima jikin nasa yabi da kallo yanaso ya gano abunda Momy ķe nufi,cikin muryar kuka ta soma magana cikin kuka tace yanzu Musayyet irin tarbiyar danai mk kenan?

Wannan shine sakamakon kulawar dana baka tin kana yaronka  harkawo girmanka?
Kafad'amin menai maka da zaka sakamin da irin wannan bak'in fetin  ?  Dama na sani nasan cewa turaka k'asar waje da Alhaj yake dole idonka ya 6ud'e ,nan ta d'urk'usa tazube kan carpet d'in dake d'akin ta soma kuka me cin rai"""" Musayyet kam sam besan abunda tk nufiba dan haka da sauri ya durk'usa yana rik'e hannunta da zimmar ze d'agata tai saurin tankwa6e hannun ta d'ago kai cikin muryar kuka tana cewa karka ta6ani ,,,karka soma ta6ani tinda ka riga ka canja Ashe a hakane kk nuna baruwanka da mata amma cikin zuciyarka ba hk bane?

Kallon fa'eza yai wacce ta k'ame a jikin mirrow jikinta se rawa yk dan batai zaton haka abin ze kasanceba.

Musayyet kuka yafara yana cewa Momy menayi dan Allah  wallahi bansan kome kk nufiba. ?
Tsaye ta mik'e goge fuskarta ta kalle shi sannan ta kalli fa'eza da sauri  fa 'eza tai k'asa dakai tana matse hannunta .

Momy tai wani murmushi me ciwo tace kana nuna kamar bakasan komai ba ko?  To muje a haka amma kasani cewa seka auri fa'eza tinda kaine wanda kafara saninta a matsayin 'ya mace """"""    inaso ka shirya cikin lokaci k'ank'ani  fa'eza zata zamo matarka.

Tana fad'in haka tai waje da sauri har tana tuntu6e sotake kawai tajita a d'akinta.

Musayyet kallon fa'eza yai ya doka mata harara memakon yaga fuskarta cikin tashin hankali amma se yaga tana murmushi""""

Kallon ta yai  cikin tsoro dan yanzu kam ya gano gadar zaran data shirya masa"""..  wani yawu ya had'iya me d'aci tana lura dashi  dan hk tai dariya tace baka had'iyi yawuba Musayyet  se randa kaji waliyammu suna cewa kazama mallakina ta har abada "" kasani cewa  duk abinda nakeso  sena sameshi kota tsiya kota arzik'i  daga ta fice tana kad'a jiki.

Tana  shiga ta fad'a kan gado ta saki wani kuka  tana shafa kan khairat wacce keta bacci abinta .

Wannan wane irin abune ?   Yau mijinta ya ni santa da ita ranar bak'in cikine agareta dan dama idonta 2 ba bacci takeba.

Gashi a ranara ne Musayyet da Fa'eza sukai mata abinda bazata ta6a mantawa ba.

Ita kam data san hk zata faru da fa'eza bata zauna  a gidan ba .

Kuka ta k'ara saki  dg k'arshe tai Alwala ta fara sallah ko zuciyarta taimata sanyi.

Fa 'eza na fita Musayyet yasa kuka ya kwantar da kansa  ajikin pillow yana dad'a k'ank'ame pillow d'in cikin kuka mara sauti """ seyanzu ya fahinci abunda fa'eza tai masa sosai yaji ciwon abun a ransa """  Abunda be ta6a yiba yau shiza ai wa sharri akan sa?   Lalle kaidin mata babbane.

Abinda yafi jin ciwo shine Momy tace seya aureta  A kowane time za a iyayin maganar auran, shikam meze da ita yarinyar da batada kunya bare mutunci.

Dama nasan turaka k'asar waje da Alhaj yake dole idonka ya bude,, kalmar data sake dawo masa kenan dan hk ya dafe kai yace ya ilahi.

Kuka yaci gaba dayi daren ranar ko runtsawa beba hk ya kwana cikin kuka da 6acin rai.

Fa 'eza kam daren ranar kamar sallah haka taita juyi akan gado  takasa bacci dan farin ciki.

A subar fari Alhaj sa'ed ya farka wanka yayi yasa coffee d'in  jallabiya yq nufi masallacin dake

gidan .... koda ya dawo kai tsaye bangaren zarah yayi ya sake knocking wajen so 3 amma shiru ' murmushi yayi ya nufi bangarensa .

Zarah bata farka ba se wajen shida na safe tana tashi ta nufi toilet brush a farayi sannan tai wanka ta d'ora da Alwala duk da cewa ba sallar zataiba amma yanada kyau ka zauna da Alwala.

Tana fitowa wani d'akin tayi wanda shima a cikin d'akin yk kaya ta sauya wani material ne coffee me ratsin adon zuma a jiki sosai tai kyau abinta duk da simple make up tayi....... kan gado ta koma ta kwanta tai lamo tana kallon adon dake jikin zanin gadon me uban tsada da kyau.

Idonta ne yagano mata phone d'inta wacce tai wurgi da ita """ tashi tai zaune ta dauki wayar se kuma ta kama juyata a hannunta tanaso ta bud'e amma tana tsoron kada wancen ya kuma kiranta.

Amma ai koba dan shiba zatai amfani da wayarta ko dan mahaifanta da kuma aysha.

Nan tasa hannu ta kunna ta gabanta n fad'uwa seda wayai tai minti goma a hannunta bataga alamar kiraba sannan ta saki jikinta gamida sauke ajiyar zuciya.

Da wurwuri Musayyet yabar gidan bayan ya shiraya kansa cikin k'ananun kaya sosai yai kyau amma kallo d'aya zakamai kagano idonsa ya d'an fad'a kad'an.

Kota kan drivern sa bebi ba wanda tin daya fito yake gaidashi amma ko kallonsa beba "" hk ya figi mota yabar gidan.

Da mamaki drivern yabi motar da kallo sbd wulak'anta mutun ba halayyar Musayyet bane.

Babban Company ne wanda a time d'in karfe 7am ma 'aikata masu goge goge ne kawai sukazo kasancewar se 8am kowa ne ma'aikaci ke zuwa .

Amma se gashi yau tin kafin time yayi Musayyet ya riga kowa zuwa """ wanda shi baya tashi zuwa se wajen 9am ko zuwa 10 .

Da sauri suka 6ude babban gate d'in me adon golden suna sara masa gamida gaisuwa """ sama sama ya amsa yai ciki suka biyoshi da laptop d'insa da wata bak'ar bag k'arama wacce papers ne a cikinta masu mahin manci.

Har office suka bishi suka a jiye mąsa sannan sk fita.

Sosai office ya had'u iya had'uwa kujera yasamu ya zauna ya kifa kansa da table yana k'wallah .

Wayarsa ta hau ruri har wajen so 4 ana biyar 5 d'in ya daga murya kasa kasa yk magana ""ok kawai yace zaku iya samuna ina nan daga hk ya aje phone d'in.

8 dede breakfast ya kammala agidan amarya zarah amma ta kas fitowa """ yunwa ce ta isheta dan hk cikin sand'a ta fito da sauri ta nufi dining .

Tea ta had'a ta zuba potatoes da waina kad'an a plate ta plantain ta soma ci.

Kamar daga sama ta hango shi ya fito  fuskarsa dauke da smile yana nufo ta"" ai da sauri ta had'iye tea d'in data kur6a tai k'asa da kantå.

Sanye yake da jallabiyar dazu setaga yayi kyau sosai kamar yaro sede shekarun dayake dasu.

Har yazo gun kanta na k'asa bata d'agoba .

Salamu alaiki ya gimbiyar mata Abumma ba gayyata ?  Da ftn sahibar tawa  ta kwana lfy a gidan mijinta. ?  Yai maganar fuakarsa ck da smile yana me jan kujera ze zauna.

Murmushi ya k'arayi yace baby ina kwana tinda baza a gaisheni ba.

Da sauri ta d'ago kai suka had'a ido setaga  yamata kwarjini bakinta na rawa tace dama dama yanzu zan gaisheka """sosai ta bashi dariya nan ya kama kwaikwayonta yanda tk magana.

Mamakinsa tk amma tai shiru   yai dariya yace to a hadamin tea nima""  cikin rawar jiki tagyad'a masa kai alamar to nan ta kai hannu zata d'uki cup  shima yakai nasa hannun ze d'au spoon aiko hannunsu ya had'u dana juna  "

Da sauri ta kalle shi shima  idonsa akanta ko kiftawa bayayi sbd wani shock yaji.

I love you  All😊
[31/08, 16:19] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBAN*

*MUTUN*

Creating  and Written by

UMMEE  MUKHTAR🎁

Kwana  2  anjini shiru  nayi d'an zazza6ine nagode k'warai  da kulawarku ina  ganin tex d'inku naya jiki  nagode  sosai sede  ba turon kayan dubiyaba🤭😂

🅿12

K'ok'arin janye hannunta tai amma setaji ya rik'e yana shafa hannun   kallon  ta yai cikin wata murya me saukar da kasala yace meyasa bakiyi lalle a hannnba ?  Dan motsi tk da mouth dinta jikinta se rawa yake duk sanyin AC dake palon amma gumi take  yi"""""""""    murmushi yayi haryanzu hannunta na rik'e a cikin nasa cup d'in ya d'auka ya soma shan tea amma be saki hannuntaba seda yasha rabin  cup sannan ya kalleta yace kona baki a bakine kingani na k'oshi """"   da sauri ta girgiza alamar a'a.

Murmushi yayi yace tatashi suje room d'insa gabantane ya fad'i  da sauri ta kalle shi  ya d'aga mata gira alamun eh'''   tsam ta mik'e   tsaye tace ya shige gaba dad'i yaji aransa dan hk ya yatashi ze rik'e hannunta tace a a suje hk tana biye dashi.

Dole yai gaba tana binsa abaya yana waigowa se su had'a  ido yai mata smile  itako duk ta takura .

Seda sukai tafiya me dan nisa ya murza key yace to muje baby na """"""   meze gani wayam babu zarah babu alamunta.

Da gudu ta shiga room d'inta ta danna key ta k'ara shigewa cen d'aya  d'akin ta haye kan bed tn maida numfashi.

Hannunsa ya had'a a k'irjinsa yana dariya yace au yarinyar nan guduwa tayi?

Murmushi  yayi ya shiga room dinsa yai wanka ya kimtsa phone d'insa ce tahau  k'ara  sallama yayi yace gashi nan fitowa  dg hk ya kashe ya fito.

Bangarenta ya nufa yai knocking amma bata bude ba  girgiza kai yayi kawai ya fita """"  yn fitowa  suka hau gaidashi mota suka bude masa sannan suka bar gidan.

Amotane driver yace yalla6ai ina muka nufa ?

Seda ya gyara glass d'in dk face d'insa yace muje gidana.

Driver  yace to  yalla6ai.

Momy sanye cikin atamfa super light pink  zaune ita da khairat a   dining  danko fa'eza bata fitoba  ""  a gogon dk manne a palon ta kalla taga 12  amma har yanzu cikinsu ba wanda ya fito "koda yk taya zasu fito  bayan sun san lefin da sukai.

Momy tacewa Khairat kije dakin ya musayyet kice yazo ina kira"""  da sauri khairat ta mik'e yayinda ta aje wainar data gutsira tace to mama  da gudu ta nufi sashen Musayyet  sede  tai Knocking  harta gaji ta dawo da gudu tace mama baya nanfa cikin muryar yara"""  Momy ta aje cup tace kinyi knocking  ba a bud'eba ?  Khairat tana k'ok'arin zama tace eh mama.

Momy da kanta ta tashi  taje taita knocking amma shiru  """ k'wafa tayi tace wato yaran nan fita yayi ko zuwa ya gaidani ma beba ?

Ya min lefi amma shize yi zuciya dani?

Bakomai zedawone.

Koda ta dawo tace taje ta kira fa'eza .

Fa 'eza na kwance cikin bargo se bacci take dan daren jiya batai bacci ba sbd murna Musayyet zezamanata ""

Anty Anty  kizo  inji mama muryar khairat kenan dk bak'in k'ofa danta buga ba a budeba.

Mik'a tayi sannan tai saurin tashi ta kalli agogo setaga  rana tayi  da sauri ta tashi tace kice wanka nk gani nan zuwa """

Khairat tace to anty .

Tana ina?   Cewar Momy khairat tace  an wanka tace wai """  murmushi Momy tayi me ciwo sukaci gaba da breakfast .

Seda ta kimtsa sannan ta fito kamar munafuka jiki duk ba k'wari ta zauna dg cen gefe tace momy ina kwana.

Kan momy nakana TV ko kallon ta bataiba tace fly  .

Shirune ya biyo baya   wanda a time d'inne Alhaj ya shigo Momy  da fara'a ta tarye shi tace ango se yanzu kaida kk tashin wuri ""  dariya yayi yace wlh fa yanzumma  sauri nk anata jirana .

Fa 'eza tace ina kwana dady cikin kulawa ya juyo yace Ify lau fa'eza ya kwanan gida?

Tace Ify lau dady "" nan yace kinbawa Musayyet paper kuwa?

Momy ce ta watsa mata wata harara wacce tasa ta yin qasa dakai tace a a a cikin rawar murya.

Yace to ai gara kibashi ko zaman hk ba dad'i nizan wuce jibi ina da tafiya kuma inaga zan 2weeks acen America so ina tinanin barin yarinyar nan hk ita kad'ai nafiso ace wani nawa haka yana gidan a zaune amma de zanyi tinani nan ya mik'e yace seya dawo.

Momy ta bishi tace Alhaj ka manta da batun 2million d'in danace maka inaso ?

Juyowa yayi yace karki damu bari na dawo yanzu ana jirana sbd ke nakasa wucewa senazo mungaisa "" dariya tayi tace a a Alhaj wasa kk kade samu yarinya kanaso kamin wayo.

Dariya yayi yace inna biyeka zan makara dg hk yai waje.

Duk fara'ar da momy take tana shigowa palor ta dauke wuta ta kalli faeza tace sekije ki karya ko in kinga dama.

D'aki suka wuce ita da khairat suka barta nan .

Ita kam ko Momy zara yanki naman jikinta bazataji komaiba burin ta yn gaf da cika.

Misalin 3pm Musayyet na kwance a office hawaye yake kansa na kallon saman office d'in knocking yaji anayi da sauri ya share hawayensa yace yes.

Nan aka turo k'ofar aka shigo yalla6ai  dama megidane yayo waya yace ya kira phone dinka a kashe .

Musayyet  ya kalli phone d'insa yace eh hakane namanta na kashe ta ""meya faru  ?

Eh dama  cewa yayi wai kaje gidansa dake cen white palace  Area B  kad'akko masa wasu papers.

Dafe kai Musayyet yayi  yai shiru cen yace to  .

Mutumin fita yayi ya rufo k'ofa .

Wai meyasa dady keson aikena gidan waccen mara kunyar Amaryar ?

Gaskiya gaskiya haba dan Allah  wlh banson zuwa dole kawai za amin.

Nan ta shi  yanufi gidan Zarah.

Zarah jin tashin mota yasa tasan cewa ya fita ba kuma ze dawo yanzu ba.

Palon ta dawo ta kunna kallo  tana k'arewa haduwar gun kallo  ""  merry ce tai sallama  tace sannu madam Zarah ta juyo tace yauwa   "" merry tace me kk so adafa yaune?

Zarah tace kawai ki dafamin shinkafa da manja da salak setumatir da albasa "' merry tai shiru dan bata ta6a yin irin girkinba duk da cewa tasan shi.

Tace to madam  nanta ta shi  ta tafi  zarah kam murna tk yau zataci abinda tafiso acikin abinci.

Kallo tk cikin kwanciyar hankali nan bacci ya d'auke amma setai rub da ciki yayinda dan kwalin dk kanta ya rufe mata fuska.

Da sallama ya shigo gidan sede shiru farin top ne ajikinsa se bak'in jeans hannunsa sanye yk da agogo fari se farin glass.

Sallam yakeyi amma shiru nan yai tsaki yace sekace gidan arna """ da gudu merry ta zo ta durkusa tace welcome sir kai ya daga mata yace are you alone ? Tace no sir to meyasa se aita sallama kamar gidan ba kowa """" tace kai hkr ina cen cikine kasan munada nisa a tsakani . seyanzu ya tino yace hakane .

Nan tai masa nunu da zarah wacce ke bacci dan kwalin rufe a fuskarta amma duk wata sura ta jikinta ta bayyana kasan cewar rigar ta matseta .

Kallonta yk sosai harda cire glasa din dk face dinsa ya ta6e baki yace baruwana da wadda ke gidan amma yanada kyau kuringa kasancewa kusa kusa sbd koda wani zezo kinganeko """ merry tace to sir

Merry tace me kk bukata yace no yanzu zan fita jeki kawai.

Tashi tayi ta koma gun aiki.

Nan ya soma taku yafara tafiya har inda zarah take ya qarw mata kallo ya ya tsine face yace koda banga face dinta ba yarinyace kuma kyakykyawa shima dady wallahi se a barshi me makon ya auro dede dashi yai tsaki yai ciki abinsa.

Dakin ya bude ya jawo drower  yaita dube dube sannan yaga papers  ya maida kofa ya kulle ya fito.

Koda ya fito bata palon bayan ta kawai yagani tana tafiya  hannunta rik'e da phone d'aya hannun kuwa dankwalin kanta ne rik'e dashi yayinda gashin kanta ya zuba har baya.

Tsayawa kawai yayi yana kallon gashin dk kanta yace anya yarinyar nan ba aljana bace karo 2 kena  sede naga bayanta amma bana ganinta .

Wata zuciyar tace masa to kai meye ruwanka da ita ma .

A fili ya furta hakane fa meyai ruwana da ita.

Yace to ai matar babanace dole naso nasanta .

Wata zuciyar tace ba dole bane.

Daga haka ya fita yabar gidan .

Ai hkr banjin dad'ine 😔
[31/08, 16:19] +234 905 934 3174: 👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBAN*
*MUTUN*

Creating And Written By

*UMMEE* *MUKHTAR*🎁.

Dedicate to (Maryam Mamee) barka da dawo wa ina tsarabata🙈😌

Masoya wannan novel inajin dadin comments dinku Allah yak'ara zumunci.😊😘

🅿13

Zarah na shiga d'aki ta kwanta kan bed ta kira wayar Aysha Amma a kashe dan tsaki tayi tace kawai seki kama ki kashe waya """ to kode batada cajine ? Wayar ta aje tasake kwanciya tai shiru tana tinanin yanda zamanta ze k'are a gidan ""

Wayar tace tai k'ara tana d'auka setaga sunan Alhaj sa'id ne gabanta ne ya fad'i hannunta na rawa tai pckcall amma tai shiru batare datai magana ba.

Yana daga kan chair me juyawa seda ya tsiyayi juice ya d'an sha sannan yai magana yace baby na wato shine d'azu harda yimin wayoko? To nima zan rama ""murmushi yayi ita kam kamar wacce aka sassak'a tai shiru se motsi tk da baki :::;;:;""" yace yade kinyi shiru Zarah kina min rowar abubuwa da yawa daga ciki harda muryarki """ yau inason kasancewa dake domin na jima ina muradin ranar dan Allah karki k'i pls I need u ya k'arashe maganar cikin salon soyaiya .

Zarah phone d'in tabi ta da kallo cikin ranta tace taf wlh bade ni zarah ba sede ka nemi wata ba ayoni dan wani dattijo yaji dad'i dani ba tai maganar cikin zuciyarta.

Yace yau zami hira me yawa kinji nan da 7pm zan dawo""" yana cikin waya ne d'aya wayar tai ringing anan ne yaiwa zarah sallama batare datace masa k'ala ba.

Yana kashe wayar zarah tai dariya tace lalle mutumin nan ji yanda yk wani kashe murya waishi yaro Lalle kanada aiki """ Ahaka zaka gaji ka sallameni .

Musayyet koda ya fita seda ya biya wani babban office ya kaiwa Alhaj papers """" waje ya samu ya zauna Alhaj sa'id yace harka tashine? Musayyet yace eh Dady banajin dad'i ne .

Subahanallahi amma ka kira doctor Safyan kuwa?

Yace a a zanje hospital d'insu idan na fita "" Dady yace idan bazaka iyaba kaimasa waya yazo mana banson kana lalura amma sekaita harko kinka bazaka kulaba harse taci k'arfinka sannan dg baya kazo kana kuka wayyo Momy wayyo Momy """"gaba d'aya suka sa dariya Musayyet yace ai yanzu nadena wannan ma ina yarone.

Dady yai dariya yace oh yanzu an girma ko?

Musayyet murmushi yayi dady ya kalle shi yace musayyet yaron mama """

Dama inaso miyi magana amma inaga se gobe idan nazo gidan """ Musayyet yace to Dady .

Wayarsa ya ciro yana danne danne yayinda Dady ya maida hankali wajen tura wasu tex ta laptop d'insa.

Number Zarah ya kira tana ringing yayinda shi kuma murmushi Shinfid'e akan face d'insa .

Zarah  na Zaune tanacin Abinci a room dan tak'ima fitowa palour dan karsu had'u da megidan.

Number de ta kuma gani aje plate d'in abincin tayi   yayin da ta tsinci zuciyarta ta dason d'aga wayar   wata zuciyar tana me ce mata kinada aure fa yazaki aikata hakan ?

Runtse ido tayi ita kam tanason jin muryar guy nan domin kuwa tana mata dad'i.

Cikin rawar hannu ta d'auka """Musayyet  yana gani  an d'aga yai murmushi ya tashi ya fita Dady na kallonsa ya girgiza kai yana smile  yaci gaba da aiki.

Cikin murya me sanyi yace my beauty  da ftn kina lfy """"  idon ta ta rufe batare da tace komai ba ya shafi kansa yana kallon korayen flowers d'in dk harabar gun yasaki numfashi yace dan Allah  ina neman  Alfarma agunki I know u can do it for me  "' pls my one don't say no.

Tin daya fara magana ta kwanta akan bed tana lumshe ido har cikin kanta voice d'insa ke mata yawo.

Sbd tanajin dadin voice d'insa .

Yace dan Allah  kifad'amin inda kike  inasonki inasonki inasonki koya ya kike ina k'aunarki tin danaji muryarki wancen karon dana kira by mistake  nakasa sukuni dan Allah kitema kan am really need u in my life   ya k'arash maganar yana share k'wallah domin wannan itace damarsa idan har be fito da mata a wannan time d'in ba Momy fa eza  zata aura masa.

Ita ma zarah k'wallah t share seda ta saita kanta sannan tai magana cikin sanyin murya "":"   kai hk duk da banganka ba nima inasonka kuma ina kaunarka amma bazaka ta6a gani naba har abada kai hkr dg haka tai saurin kashe wayar gaba d'ayanta ta dira kuka .

Musayyet wayar yabi da kallo kamar wani yaro face d'insa ta canja se hawaye dk zubo masa yn gogewa kansa ya kifa a karfen silvan dk wajen yana numfashi sama sama .

Jin shirun yayi yawa ne yasa Dady fitowa nan ko ya ganshi se numfashi yk sama sama """   da

sauri ya dafa shi yace oh my GOD  jikinne ?

Nan musayyet ya d'ago kai ya rungume Dady yasaki kuka """"  mamakine ya kama Dady na ganin Kukan Musayyet  yaron  da rabonsa da kuka tin yana shekåra 7..

Hankalin Dady yatashi nan yakama shi suka koma ciki ya zaumar dashi akan sofa yana shafa kansa yace my son menene damuwarka ko jikinne ?

Musayyet cikin kuka yace a a Dady  bata sona ne kawai kuma narasa  inda take ""  Dady ya sake kallonsa cikin rashin fahinta yace itawafa?

Musayyet  yace bansan taba dady amma nayi nayi tafadan inda tk tak'i .

.murmushi  dady yayi yace inna fahinta budurwa kayi kenan?

Da sauri Musayyet ya d'aga kai Dady ko dariya yayi harda cire hula ya aje kan center yace my son karka damu idan na dawo dg tafiya zan nemo mk duk inda tk kuma zami magana da iyayenta ka kwantar da Hankalin ka  kamar ta zama matarka.

Dady yace mene sunanta Nan Musayyet ya danyi murmushi yace nima bansani ba tak'i gayamin.

Wata dariyar Alhaj Sa ed yayi yace kafiye shiririta  wace wannan tk garamin d'a haka.
?

Kaga maza tashi kaje gida nima ina hanya yanzu   "" nan musayyet ya mik'e  cikin murna yana k'ara goge face d'insa.

Alhaj yabishi da kallo yana dariyä.

Zarah kam sosai hankalinta ya tashi akan wannan saurayi me dad'in murya tashi tayi tashiga kai kawo cikin room d'in tana tino kalamansa .

Tabbas ya shigo rayuwarta kuma da alamu zeyi nasara akanta tinda gashi tafara sonsa wannan wane irin abune ya ilahi ta furta tana me dafe kai.

Musayyet cikin farin ciki ya dawo gida su Momy na palour banda fa 'eza dan tana d'aki.

Duk murnar da yake yana shigowa ya maida kayarsa Momy na ganinsa ta dauke kai "" da gudu khairat ta nufe shi tana oyoyo ina ice cream d'ina ?

Idonsa akan Momy amma ko kallonsa bataiba y dauki khairat yace yanzu zamu fita muje musiyo ko.

Tana hannunsa ya nufi inda Momy take ya durkusa yace momy ina yini.

Juyowa tayi ta tsareshi da ido tace eh ai ka isa kaima kanajin kanka namijine ka kawo k'arfi harda zk fita batare da kazo ka gaidani ba """ ya maka kyau .ta maida kanta kan TV wanda suke cartoon .

Cikin ladabi yace wlh momy ba hk bane inada aikine sosai amma kiyi hkr.

Cikin sanda yataso ya kwanta dede kusa da ita ya kashe fitilun dk d'akin yai mata Addu'a sannan ya kwanta Amma ba bacci yakeba idonsa biyu

Kusada ita ya matsa ta yanda ze iya jin numfashinta yasa kansa dede face d'in ta yn kallonta har bacci ya d'auke shi.

Cikin dare Zarah na motsawa taji Alamun mutunn dan hk tazabura tana neman inda fitila d'akin take ta kunna wacce ke jikin bed"""jitai an riketa gamida jawo ta zuwa jikinsa ya rungume yana shafa kanta cikin murya k'arama yace yace is ok nine tare dake ba waniba """ki kwanta baccinki nasan kin gaji da yawa kina bukatar hutu.

Zarah duk da sanyin d'akin amma seta gama gashi de ta gane me muryar amma rungumar dayai mata ne yasata shiga wn irin hali tai shiru tana mots jiki alamun so take ta kufce masa. Yagane nufinta dan haka yai murmushi yasake rungumeta ya kwantar da ita kan k'irjinsa yana shafa kanta gamida shafa bayanta idonsa rufe yayinnda Zarah idonke bud'e tanajin yanda yake mata ruge idonta tayi tana shakar kamashin jikinsa harbacci amma sam takasa bacci.

Jin tayi shiru kuma da alamu idonta 2yasashi kwantar da ita gefensa shima ya matsa dg gefe ya kwanta yn murmushi.

Daren ranar kowa be bacci ba se s'aka da warwara har Asubah tagabato ya tashi ya bar d'akin .

Jin ya fita yasata bud'e ido ta tashi taje tai saurin saka key sannan ta shiga toilet dan yin wanka da alwala.

Dan Allah kumin Uziri wani Abune yatasomin cikin gaggawa zakujini shiru Amma ran lahadi zanci gaba insha Allah .👏🏻

⚜BRILLIANT WRTS ASSO🖊️

👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

*AURAN* *BABBAN*

*MUTUM*

Crtg And Wrtn By

_UMMEE _MUKHTR🎁__

🅿44

Brush tayi sannan tai Wanka ta goge jikinta sannan tai Alwala ta fito babban room d'in wanda yk gari guda gashi ya tsaru komai ruwan golden ne""" tsaye tayi tana k'arewa room d'in kallo ,,,A hankali tafara bin wani corridor nan ma wasu rooms d'in tagani a kukkule tasa hannu ta bud'e"" d'aya bayan d'aya tabi rooms d'in tana kallo yayinda taga kowanne adonsa dabanne hakama gado dake ciki da komai da komai """ sannan duk akwai toilet ciki da bayn rooma d'in kuma ga ventilation nan da flowers se kad'awa suke.

Kowane room akwai AC cikinsa da kayan kallo da komai na morewa rayuwa.

Ajiyar zuciya tayi sannan ta dawo room d'in farko ta maida doguwar rigar jiya da Aisha ta bata dan ita kadaice tasan zatai sallah duk cikim kayanta tinda Momy ta riga data sako mata k'ananu.

Sedata k'ara kallon k'ofar da Musayyet ya fita tai murmushi had'i da rufe face sannan ta tada ik'ama .

Shi kam tini  yai wanka har yai Sallah kaya ya canja sannan yajawo  system  d'insa yafara tura sak'onni zuwa nigeria .

Magenshi ce tai tsalle ta hayo kan bed d'in  gamida shigewa jikinsa ta kwanta tai luf ta zurawa system d'in  ido kamar tasan Avunda yakeyi.

Murmushi yayi had'i  da shafar kanta ta k'ara lumshe ido yaci gaba da aikinsa.

Seda rana  tafara d'agawa sannan ya fito dg room ya nufi tafkeken kichen dan sama musu abunci.

Yana zuwa ya bud'e  firij ya fito  da kaji wanda suke a yanke yasoma sarrafasu.

Ganye wajen kala 5 naga ya yanka harda carrot  da koren tattasai  harma da yellow Albasa da attaruhu  ""farfesu yayi dg k'arshe ya zuba kaya kayen gamida zuba   blue d'in  wani sinadari nan take kazar ta canja launi zuwa blue  """ dairya yayi dan yadan abinda ze faru dg k'arshe.

Tea ya hada tareda gan yaiyakinsu  da citta kanumfari sannan ya tace ya zuba a flask ya soya potatoes  yakai dining  ,,,madara ya dakko tareda kayan shayin wanda duk nasune irin na cen ya je a dining.

Zarah kam rigar ta cire tasamu wasu kayan tasanya wanda suma duk uwar d'arince """"  gaban mirro taje ta zauna  ta shiga zuba makeup  """"""body spray ta fesa sannan ta koma cen cikim wani room  wanda bash ta kwana  ba ta shiga ta kwanta kan bed tana juyi cike da farinciki""" Shiru tayi tn kallon room d'in  up  and down  .

Da sallama yake knocking amma shiru wani key yasa ya bud'e  room d'in  ya tura k'ofar  yn murmushi

Be ganta anan ba  dan hk yaqara shiga ck.

A bud'e  yaga k'ofar  dan hk ya la6e yn kallonta .

Tashi tayi ta dakko remote ta kunna kallo ta dawo kan bed ta kwanta.

Yana  kallon yanda jikinta ke motsi yai smile cikin ransa ko tinani yake taya ze shiga  dakin Alhali tn sanye da wa'yan nan kayan?

Tsayuwa ya gyara sannan yai sallama ya shiga"""" tana ganinsa tai saurin kwanciya gamida janyo bargo ta rufe dukkan jikinta ta runtse ido azuwan bacci take"""

Murmushi  yayi cikin ransa yace k'uruci kenan sedana ganki sannan  zaki kama jaye jayen bargo? Ya fad'a yana nufar inda tk.

Yana zuwa ya shige cikin  bargon ta rufe ido tana d'an matsawa nesa dashi.

Smile yayi sanna ya k'ara daf da ita ya rungumota gamida d'ago face d'in ta suka fuskanci juna tai saurin  kwantar da kanta kan k'irjinsa tana nok'e nok'e""   dariya yayi yarad'a mata a kunne A hankali yac waime kk 6oyemin  ne ?

Shiru tayi daga nan yaci re bargon ya d'aga ta cak ya rungumota idonta rufe  a k'irjinsa tasak'ale hannayenta zuwa wuyansa shiko kallonta yk yn smile har suka fito palo  """ be ajeta ko inaba sekan dining  ya matso da  chair d'in sa dede tata har yanzu idonta na rufe tasa hannaye 2 ta rufesu.

Har gabanta yazo ya cire hannayen nata gamida busa mata iska a ido yana kaiwa kowane eyes d'in ta kiss .

A hankali ya bud'e  sukai Arba da juna.

Tai saurin sunkuyawa tn wasa da hannunta ya durk'usa dede kan k'afarta yana shafa dogwayen

Iap d'in ta "" hannu tasa zata cire hannun nasa yai saurin rik'eshi  da d'aya hannun.

Sabahul  khair ya habibty murmushi tamasa tn cigaba da wasa da  hannunta Shima murmushi yayi ya shiga hada  mata breakfast.

Yana bud'e  farfesun kazan Zarah ta d'aga hanci gamida bud'e ido nan suka hada  ido da Musayyet ya d'aga mt gira batai magana ba sede smile   cikin ranta tana cewa wannan wn irin abuncine haka gashi  yai blue ga uban ganyaiyaki.

A hankali  ya zo daf da ita yasa kujera dede saitinta yafara bata abaki.

Tinkafin ta tauna  taji zuciyarta na tashi da gudu ta nufi toilet shima da yabi bayanta yn dariya.

Tana zuwa ta zubar dana bakinta ta wanke mouth d'in ta"""""" jitai an rungumeta ta baya yana dariya yace baki ta6a ganin irinsaba ko?

Shiru tayi tanajin yanda  yake shafa mata ciki kamar ya samu wata fulawa"""   juyowa tai zata fita  ya rikota suka hada jiki.

Kallonta yake yn tinane tinane shikadai aransa.

Kanta a k'asa tace inason shirt d'in jikinka  ta fad'a  cikin muryar  shagwa6a.

Face d'in ta yad'o yace kinsonta?   Kai ta d'aga masa kawai "" Aiko Musayyet  ya cire white shirt d'in sa ya bata """gani yai kawai tahau sawa lokaci lokaci tn kallon kwantaccen gashin k'irjinsa wanda yai kama dana Arab """  kallonta  kawai yake yn smile harta gama  sawa sannan ta zura da gudu tai hanyar daki Shima da gudun ya bita yn dariya  yana cewa seta bashi shirt  d'insa

Ayshan  Nigeria maganar Auranta da Naseer tayi k'arfi dan har an turo ansa lakoci  duk da Mahaifiyar  Naseer bataso abunba dan sotai ya auri Aneesa Amma Minister yace Abunda D'ansa keso shima shiya keso.

Naseer ne ya nunawa Hajiyarsa pic d'in  Ayhsha  Abun mamaki tin data ganta taji tanason yarinyar """"nan tabaiwa Momyn Aneesa hkr """ Sannan ta shiga tsare tsaren biki.

Uhmmm Mulabi kinga yaron nan koya kiramu ya gaishemu wato shi  yazama   me matako  "" yafad'a yana 'yar dariya.

Momy tace wlh fa nina daukama yakiraka "" Dady yace inafa .

Dariya  sukai gamida yi musu ftn Alkhairi.

Kubiyoni Sannu sannu Ankusa gamawa👌🏻💞💞💞💞💞💞💞💞💞💞💞💞

⚜BRILLIANT WRTS ASSO🖊

👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

AURAN BABBAN

MUTUM

Crtg And Wrtn By
_UMMEE_ _MUKHTAR_🎁

🅿45

Yau kwanansu 3 kenan tsakanin Musayyet Da Zarah sede suyi wasa,, yayinda kowa kunyar

d'an uwansa yakeji.

Kullun kayanta kenan k'ananu sbd su kad'ai gareta """Aduk sanda yaganta hk takan tayar ms da hankali ne gashi besan ta yadda zefara mataba sbd wata irin nawinta da kunyarta yakeji.

Yau ma yana kwance a room d'insa ya shiga tinani wayarsa tai k'ara be kalli inda takeba hannu kawai yasa ya d'auka yace hello.

Jiyai ance my son ya kk "? Da sauri ya tashi zaune yana shafa kai da murmushi yace lfy lau Dady ya Momy?

Dady yai murmushi yace tn lfy """ ince de kunje shopping d'in?
Musayyet yace a 'a amma anjia zamu """ to yakamata kuje kasan bawasu kaya ta taho dasuba "":"..
Musayyet yace hakane insha Allah zamu anjima.

To kagaidata se ajima.

Nan sukai sallama "" shikam Musayyet ya d'auka itace keson k'ananun kaya shiyasa bece mata komaiba .""""yana tashi wanka yayi yasanya k'ananun kaya ya feshe jikinta da turare gamida gyara gashin kansa sannan ya d'auki key ya fito palo.

Kai tsaye room d'in ta ya nufa se yaji k'ofar a bud'e """ shiga yayi nan ya ganta kwance da alamu bacci take abinta.

Murmushi yayi kawai ya zauna yana k'are mata kallo "" shikam ba abinda zecewa Dady se godiya .

Sanye take da riga 'yar k'arama iya gwiwa pink ce me siririn hannu gashin kanta ya zuba kan pillon datake kwance """ A hankali yafara jan yatsun k'afarta cikin k'warewa kamar yana mata tafiyar tsutsa """ murmushi kawai yaga tanayi cen kuma takama dariya amma har ynz idonta rufe yake"""" kwanciya ta gyara taci gaba da murmushi ,,,,,,,, yanda tk motsa mouth d'in ta yasa Musayyet sha'awar yi mata kiss.

Jitai kawai ana shan lips d'in ta da sauri ta bude ido sukai ido 4 dashi.

Cikin jin kunya ta tashi ta ruga zata gudu ya rik'ota yn smile gamida shafa kanta yace ki shirya

inajiranki a palo zamu fitane """ daga hk ya ya kumayi mt kiss ya fita yanajin farin ciki aransa.

Hanyar daya fita tabi da kallo tana murmushi had'i da shafa lips d'in ta tana kallo yanda yadingai mt kiss """" smile tayi snn ta shiga wanka.

Cikin minti 30 ta shirya ta sanya doguwar rigarta """ba wata kwaliya tayiba amma tayi matuk'ar kyau .

Tana fitowa ta tsaya jikin k'ofa tana wasa da hannunta ...

Danna waya yake kawai amma seyaji alamun motsi yana d'aga kai sukai ido4 da fara'a yataso har inda take yace wow my beautiful wife kinyi kyau fa """hannunta ya kama sukai hanyar farfajiyar gidan tana kallon yanda gidan yk da girma .

Wata farar mota suka shiga ya bud'e mt gidan gaba ta zauna sannan ya shiga suka tafi.

Tinda sk taho Zarah ke kallom yanayin k'asar abun sha'a wa haka suke da tsari ga yawan shuke shuke .

Yana kalle da ita yn murmushi har suka iso Attahrah Mall """"Babban mall ne wanda ba abunda babu ciki kama dg abunci konasha kayan sawa provision kayan kwalliya komai da komai de.

Ma'aikatan gun duk larabawa ne nan ya shiga jidar mata kaya kala kala riguna dogwaye masu rasha rasha dana nau 'in larabawa.

Tana biye dashi yayinda itama tk diban duk abinda yai mata .

Kayan makeup ta diba da wasu rigunan se kayan ciye ciye.

An kashe kudi me yawa wanda harseda aka kawo musu kayan har motarsu .

Kai tsaye OLD CITY COPIC CAIRO Suka nufa wanda anan ne kayan tarihi yake tinda cen Zarah tayi kallo yayinda idan taga wani abun na tsoro seta k'amk'ame Musayyet.

Basudawo ba se yamma lik'is suna dawo wa salla sukai sannan Musayyet yace yau tare zasuyi griki.

To kawai tace bayan mintuna kad'an sk shiga kichen jollp d'in taliya ta dafa yn kallonta kamshi duk ya cikashi zaune yake kan kujera bayanta kawai yk qarewa kallo yanda tk da kyan diri.

Juyowa tayi yai saurin kau da kai tai smile tace nagama.

Tsaye ya mik'e yn smile ya kalli jollop d'in wacce tasha kifi yace amma kin iya girki muje muciko.

Kai tsaye dining sk zauna sk faraci tana kallon yanda yakecin abincin da alamu yanajin dadin sa.

Kallonta yayi yace na tambayeki?

Kai kawai ta d'aga masa yayinda ta aje spoon d'in hannunta.

Musayyet yai murmushi yace yaya akai kika had'u da Dady na?

Murmushi tayi ta kalli kan dining d'in tana motsa mouth d'in ta .

Shima smile yayi yace inajinki .

Zarah tafara magana kanta na sunkuye tace watarana ne ina chart a Facebook a time d'in

k'aramar wayace dani"""
Se naga anturon da frnd rqrst sena amsa"""" sunan dana gani shine Sa'ed Ibrahim sunan beyi kama da wani Babban Mutum ba .

Ahaka muka fara gaisawa cikin mutunta juna lakaci lokaci harta ka gai da munayin waya . Koda mike waya dashi muryarsa bazata tabbatar mk da cewa yanada shrekaruba.

Seyace na bashi whasap number na nikuma bandashi..
Sbd banayi banida babbar waya.
Kawai abun mamaki muka fara soyaiya dashi"""musayyet yai gyran murya suka hada ido da zarah yai murmushi itama tai masa sannantaci gaba da bayani.

Harta kaiga yace nai masa alkawarin aduk yanda naganshi zan aure shi"""" ni kuma na amince

Kawai seyace zezo gidammu "" anan ne zarah tai shiru tana kallon Musayyet""" ga mamakinta setaga yn murmushi yamaida hankalinnsa gareta.

Taci gaba da cewa ni kuma bana zance se dawani wanda ake kira da kabeer.

Amma sbd mumsaba bazan iya hanashiba sena bashi address .

Watarana ran Asabar da yamma kawai senaga banana ya shigo da sauru gida yana cewa ina kike ina kike.

Da alamu ni yake nema """nida Ammi na muka fito yace zarah ina kika samo babban mutun haka gashi cen waje yana tambayar gidanku """ na tabbata koda bansan shiba alamu sun gwada shidin babban mutun ne "Zarah ina kk samo shi?

Nai shiru nace wlh baba banta6a haduwa da mutun irinsaba nide bansan shiba.

Babana yace aiko sena fita tinda har yazo gidammu dole na fita.

Haka na fito waje naganshi Zaune cikin Mota me tsada na tsaya ina tinani inda nasan shi amma

nakasa.

Fitowa yayi  yai min sallama na amsa gamida gaidashi  """ jinai ya ambaci sunana nace ina kasanni?

Yar dariya yayi yace nine Sa ed wanda mike gaisawa a fcbk.

Murmushi nayi alamun ban yadda ba domin muryasa bata nuna cewa shidin babba bane.

Wayarsa yaciro ya nunamin duka chart dimmu sosai nai mamaki tabbasa wannan chart d'in damikeyine .

Da mamaki nace masa dma kaine?

Yai murmushi yace nine zarah idan har kin yarda zaki aureni wlh inasonki tinda naga name d'in ki a fcbk naji koda ban gankiba  hankalina ya kwanta dake.

Nai murmushi  nacekai hkr ni bansan kayi sa an babana ba """bazan iya aurankaba.

Haka yaita lalla6ani dg  karshe yabani waya a kwalinta me tsada harda kudi a wata karamar jaka duk naki amsa nayo cikin gida.

Ina shigowa wani yaro ya shigo dauke da wayarda kudin yae gashi  wai agayamin yatafi seya dawo......

Babana ya fito dg toilet ya tambayeni wayeshi  batare da tsoroba na basu labari """babana najin haka yace aiko inde yadawo sena fita kuma wai shi hankakinsa ya kwanta dashi inde yace ze fito toshi zan aura.

Musayyet  yai ajiyar zuciya ya kur6i jiuce sannan yai murmushi  yace ashe duk ni yakewa yak'in  auranki.

Murmushi zarah tayi ta kalli agogo taga dare yafara tace bacci nakeji.

Musayyet  cak ya d'auketa ya aje kan chair 3st yace sekin gama bani  Ibr snn zaki  bacci
.

Smile  tayi tace ai shikenan fa nagama""" Musayyet yace no akwai saura  mana.

Ya kwanta da kanta kan lap  dinsa yace pls Zarah you should continue dis beutfl stry.

Tai murmushi tace bayan yadawo besameni ba  se babana sukai magana yace  wai yabashi ni """" ina dawowa dg islamiyya   babana yace wai yazo bana nan .

Haka de akaita abu daya ina banaso shikuma befasa zuwa ba alokcinne kabeer yai tafiya  aiko abba na yace  dady y fito .

Anan  ne ya turo akai magana  had'i da sa lokaci harde akai auran.

Musayyet yai murmushi yace ni kuma a sannan ne nakira kikai min rashin kunya ko?

Dariya zarah tayi tarufe ido yasa hanni ya bud'e  tafukan hannunta yana meyiwa idonta kiss
.

⚜BRILLIANT WRTS ASSO🖊

👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️👳🏻‍♂️

_AURAN _BABBAN__

_MUTUM_

Crtng And Wrtn By

_UMMEE_ _MUKHTAR_ 🎁

🅿46

Tasa hannu ta janye hannunsa tana mik'a gamida tashi tsaye """shikam kallonta yakeyi yn smile ya mik'e ya d'auketa nan takama dariya tana wuntsil wuntsil gamida k'ank'ameshi .

Be direta ko inaba se kan bed wanda ke cen k'arshen d'akunan ya kwantar da ita yaname zame rigar dk jikinta """ idonta ta rufe ""ya zubawa surar jikinta ido a hankali yafara shafar jikinta yana shak'ar k'amshin jikinta ,,,tin daga kan yatsan k'afarta yafara shak'ar k'amshinta har ,zuwa wuyanta ""ya d'ago kanta har ynz idonta rufe """"jitai ya cire mata brezia tasa hannu ta rik'eshi tana kokarin mikewa .

Da sauri yajawota ya kashe fitilar d'akin ya shiga yi mata kiss """" Ita kam kunya duk takama ta damma ya kashe fitila"""""" A hankali yafara lasar kan breast d'inta ta k'ank'ameshi shiko kallonta yk yana smile ya dakko duka hannunta ya zuba a gadon bayansa ya rungumeta """"ita mamaki take koma kunyarta bejiba yake mata haka.

Haka yaci gaba da abinsa sede da k'yar yasamu way se sambatu yake Zarah ihu kawai take tana dukan bayansa """sosai ya fita hankalinsa se kiran sunanta yake itako ihu take tana cewa nicefa Momynka haba dan Allah wayyo na shiga uku""" besan tanaiba harya gama ya rungumeta yana ajiyar zuciya """kuka take shiko ya rungumeta yana shafa bayanta yana me rad'a mata a kunne cewa """sorry bazan sakeba dena kukan kinji hubbi na am so sorry.

Zarah shashshekar kuka take tana k'ara shigewa jikinsa dan wani sanyi takeji na shiga jikinta .

K'ara rungumeta yai ajikinsa yana jijjigata yayinda hak'oranta se  karkarwa suke tana hawaye.

Jiyai jikinta yayi zafi  dan haka ya kunna fitila nan yaga se rawar sanyi take ya sakko kan carpet yasa  sutturarsa jikinsa na rawa yajawo drower ya dakko magani da ruwa yazo har kan bed d'in ya tallafota ya jinginata jikinsa yabata bakinta na rawa ta had'iye ya maidata  ya kwnatar ya aje cup d'in  ya dawo cikin bargon ya rungumeta yana shafa bayanta har bacci ya d'auketa .

Kiran sallan dayajine ya tashi ya shiga toilet ya dawo da kallonsa gareta har ynz bacci take dan dama shi ba baccin yaiba idonsa 2 dan koya tai motsi seya k'ara maidata jikiňsa   yana shafa gashin kanta.

Bayan yama wanka yai Alwala ya nufi masallacin dake kusa da gidan bayan an idarne ya zauna yai Musu Addu o in zaman Ify me d'orewa tare da k'aunar juna na har abada.

A kan hanyarsa ta tafiyane yake tinanin Zarah yanda ta dinga cewa yai hkr itafa Momyn sace """"""  wata 'yar dariya yayi ya zuba hannunsa cikin jallabiyarsa yana shak'ar iskar dake busawa .

Mamakine ya rufeshi jin yadda Zarah ta kasance  a matse wanda duk a tinaninsa ya dauka tini Dady ya santa """ Wani farin cikine ya rufeshi ya durkusa har kasa yana yiwa Allah godiya  daya kasance besanta d'iya maceba .

A hankali  ya shiga room d'in  nan yaganta ta farka tn kokarin tashi se cije lips take """ dasauri ya nufota tana hangoshi tai saurin taro bargon dk jikinta ta koma ta kwanta"""" murmushi yayi ya isa inda dk yace morning my habibty ya kika tashi ?

Tana jinsa tai shiru ya kwanta dede saitin face d'in ta yai mata kiss yn me mata murmushi tai saurin  juyawa ya kamota yace  haba baby na nafa bada hkr tin jiya .

Zarah ta cuno baki tace nika  fita wanka zanyi""" to maganar cikin shagwa6a  """   murmushi yayi yace to meye banganiba baby na ke tawace dama duk abinda ke jikinki koba nawaba ne?

Ido ta rufe yasa hannu ya janye hannayent ya dauketa se toilet.

Bahon wankansu ya cikashi da ruwan zafi wanda ya kwanto dg dispenser ya zuba dettol yasata ciki ta saki k'ara yasa hannu yana danna mata gun tai saurin janye hannunsa""" ga mamakinta se taga shima  ya shigo cikin bahon  ya cire kayansa ya shiga gasa mata jikinta ko ina itako se tureshi take waiya fita.

Jitai ya janyota jikinsa kasancewar akwai santsi bahon nan ta taho suww har jikinsa ya had'a ta da nasa jikin ya shiga danna mata gun se kara take ya had'e bakinsa danata ya kuma kunna shawer ruwa yadinga sakkowa kansu .

Basu suka fitoba seda sukai awa sannan sk fito tai   sallah shiya gyarata yasanya mata riga karama iya gwiwa ya daure mata gashin kanta da  ribon yasa mata tirare  duk tana  zaune tn kallonsa se kallonsa take cikin ranta tana mamakin Musayyet azatonta zeji kunyarta tane baze ta6a iya kwanciyar   Aure da itaba""" se gashi ba hakan bane.

Jitai ya bushe mata ido ya sakar mt smile ya dauketa be direta ko inaba se a palo.

Yana ajeta ya ruga kicin da gudu tabishi da kallo dariya takama ta  da kyar ta mike ta bi bayansa dan ganin abunta zeyi.

Tana shiga ta ganshi komai sauri sauri yakeyi Allah Allah yakeyi komai ya hadu na breakfast dan kada Zarah tafarajin yunwa.

Tana bayansa se murmushi tk  shiko besan da shigowarta ba se zarafin gabansa yake.

Tea ya dora yayinda ya shiga soya kwai be gama suyar ba tea d'in ya fara zubowa alamun tafasa yai saurin aje spoon yana kokarin saukewa """"" juye tea d'in yayi a flaks nan yaji wainar tafara k'onewa ya juyo gunta da sauri dan kashe gas d'in """"jiyai kawai ana dariya ta bayansa ya juyo nan yaganta tsaye yai dariya gamida rik'e k'ugu yace wayace ki taso? Tai murmushi tace nazo naga me kakeyine.

Yai tattaki har gabanta yaja hannunta ya maidata palo yace in kika dawo nida kene """ ya koma yana waiwayenta itako se dariya take masa.

Cikin mintuna yagama komai ya dawo ya jera musu a dining  zata mik'e  yai saurin zuwa ya dauketa tai masa kiss cikin muryar shagwa6a tace to waini ba abinda zanyi kenan ?

Ya kalleta  ya daga mata gira hadi smile yace akwai a binda zaki amma semun gama breakfast abun danai miki jiya ke kuma yau shi zakimin.

Da sauri ta zare ido tana kokarin sakkowa ya k'ara  matseta yana dariya.

⚜BRILLIANT WRTS ASSO🖊️

_AURAN _BABBAN__

_MUTUM_

Crtng And Wrtn By _UMMEE_ _MUKHTAR🎁_

🅿47

Nide ban iya ba ni kunya kake sani in kana min haka,  Zarah ta fad'a tana turo baki""" Kallanta yayi ya girgiza kai yace kenan nine mara kunya ko?   Murmushi tayi tace a'a bakai bane """" dariya tabashi  yace zakisan banda kunya yarinya""" d'aukanta yayi ya ajeta kan dining  yafara bata abaki tana kau dakai wai ita batajin yunwa.

Kallanta yayi se kuma ya kifa kansa a cinyarta ya kama kuka""""  Zarah tai saurin d'ago kansa tana menai maka  dan Allah kai hkr zanci """ tana  d'ago kansa se taga yakama dariya yana ja mata hanci  yace ashede kindamu  dani.

Murmushi tayi  yaci gaba da bata harta k'oshi  yayinda shima yace lalle seta bashi sannan zeci in bahakaba sede ya zauna da yunwa.

Haka ta bashi harya k'oshi "":"kai tsaye hannunta  yakama  suka nufi room d'insa kasancewar batayo sashenba tin zuwanta hakan yasata kalle kalle tana yaba dukkanin gidan cikin ranta.

Akan bed ya kwantar da ita yajawo drower nan taga ya fiddo da sabuwar waya iphone7 yasanya mata sabon sim ya  mik'a mata.

Ta tashi zaune ta amsa  tana juya phone d'in tace wayar waye ?
Kansa ya d'ora kan kyawawan legs d'in ta yai smile yace takice seki saka numbers dk d'aya phone d'in ki kira ku gaisa .

Murmushi tayi tace amma fa inada waya kuma bata wani tsufa ba shine zakase wata?  Kansa yacire dg legs d'in ta ya kar6i phone d'in ya aje gefe ya kwantar da ita suna kallon juna yasa hannu yana shafa lips d'in ta yace wannan bakin yacika tambaya da yawa idan sayake cewa wani abun game da wayar nan zega yanda zami dashi .

Murmushi tayi ta d'aga masa kai alamar bazata sakeba .

Nan ya shiga yi mata kiss tana zillewa yana mata cakukkulu tana dariya  shima dariyar yake be auneba yaji itama tafarai masa yai saurin cikata domin sosai abinda tai masa yasa shi dariya yanajin kamar tana mai tafiyar tsutsane a jiki.

Dariya yake tana binsa yana zagaye room d'in yana bata hkr waiya dena, itakam yanzu tasamu abun yi na korarsa dg gunta danta fahinci inde suna tare baze barta ta hutaba.

Cikin sa'a takamshi suka zube kan bed tashiga yi masa yana dariya yana k'ank'ame jikinsa da hannayensa"""

Daga k'arshe Allah yabashi sa'a ya kamata ya kwanta jikinta yashiga romance d'in ta"""" Zarah jikinta yai sanyi takasa koda motsa hannuna ne be bartaba seda yasakeyi kamar na jiya sannan ya rungumeta ya d'auki karamin remote na kunn A.C  ya kunna nan bacci ya kwashe su.

Be farkaba seda rana tayi shiya fara tashi yai wanka gamida  sallah.

Kayan breakfast d'in ya kwashe ya wanke su ya gyara ko ina yai turaren wuta gamida fesa Airfreshner  nan da nan ko ina ya d'auki k'amshi .

Komawa yayi ya tashe ta gamida murza mata yatsun k'afarta harta bud'e ido""""""   Tana bud'e wa sk hada eyes tai saurin rufe kanta da bargo yai dariya yana janye bargon yace fita zamiyi ki wanka ki sallah ko nazo na mikine?

Kai ta d'aga masa shiko smile yayi cikin ransa yace lalle kinfara cire kunyar dake tare dk my hubby dama hk nakeso.

Wanka yai mata se raki take a wai yana mata da zafi shiko idan yaji tace hka seya ja matakan brest d'in ta cikin wasa haka zata saki kara shiko yaita dariya abinsa .

Bayan yagama mata wankan ne yadawo palo ya zauna yayinda ta nufi room d'in ta dan shiryawa.

Doguwar riga ta sanya sky blue me red stone  kananu ba k'aramin kyau tai mataba abinla da fara sallah tayi sannan ta sheka makeup tai rolling ta dauki handbag ita light blue """ tana shirin fitowa ta ganshi yana shigowa room d'in sukai kari da juna """ tsaye yayi yana kallonta Allah yayi halitta anan batada maraba da larabawan k'asar Alqahira .

Iska ta busa masa a ido yai saurin kifta ido ya d'auketa cak yai palo da ita yana juyata yace kinfa k'ara kyau hubby na what's the secret?

Murmushi tayi kawai tana kallonsa "" ajeta yayi yace tahau yagoyata .

Zarah cikin jin kunya tace haba de goyo kuma?

Tsaye ya mike ya harde hannunsa akirjin sa yace koki hau ko yanzu ki sake wani wankan.

Ido ta zare tana bud'e  mouth ya d'aga mt gira yes inde zaki dingajin kunyata to zaki zama agwagwa agidan nan domin zanta saki abinda zaki wanka tin daga safe har dare.

Zarah ta rufe baki cikin muryar kuka kuka tace wlh nadena zanyi"""" zan hau bayan naka sunkuya to.

Dariya yayi yalakuce mata hanci ta sunkuyar da kanta tn dariya """ya sunkuya ta hau yaji laushin  jikinnta har cikin ransa  ya lumshe ido ya mike tsaye shibe gaba ba shibe baya ba.

Ta rank'wafo da kanta zuwa wuyansa tai masa kiss
Ya K'ara rufe ido nan take yaji tai masa cakulkuli ska zube kan chair  3st yana kyalkayle dariya itama hakan dariyar take tanaja dabaya ya kalleta yana shafa kai yace wato kingano abinda ke sank dariya sosai ko kuma abinda ke kashemin jiki.

Zarah tai magana yai saurin kamota yana  shashshafata tana zillewa ,wayarsace tai k'ara yace oh no waye ze shiga rayuwata ina cikin jindadi na?

Zarah ta maida dariyarta tana gyara rolling d'in kanta wanda  ya zame Musayyet ya d'auki phone d'in  "ga mamakinsa sunan Dady yagani yai saurin rufe mouth yace kai ashe DADY NE """

Zarah tai dariya  gaimda  nufa hanyar waje.

Musayyet cikin ladabi yace Dady na inakwana """Dady yace Ify wai yaushe rabonka da zuwa company ni ne ?  Se waya akemin anason ganinka wai ka kashe wayoyinka ko amrcin akeyine?

Musayyet ya rufe baki cikin jin kunya yace a a Dady banji dadi bane shiyasa amma yanzu zanfita.

To Allah yasawake my son amma you should take care yourself duk da inna fad'a baka daukan abin da serious.

Musayyet yai  Murmushi  yace  insha Allah  zan kiyaye Dady.

Sallama sukai Musayyet ya fito farfajiyar gidan amma bega Zarah ba.

Baya ya zaga nan yaganta bakin swimming pool ta zura legs d'in ta tana wasa da ruwan se dariya take.

Murmushi yayi ya kara gun  yace wasan ruwa ko?

Ta d'ago kanta sk hada  ido ta mike tsaye gamida girgiza kai tace a a .

Smile yayi yace zaki koyane tinda kina tare da agwagwa """ dariya yabata sukai dariya ya rungume jikinsa suka jufi wajen aje motaci.

Wata bakar mota sk shiga suka nufi Al Ansar bufekkti hotel.

Wajen shiru kamar bame rai se tsuntsaye da shukoki dk kadawa wajen ya hadu iya haduwa

bene ne wajen hawa 12  wanda ko wani room kudinsa ya kama kimanin 100k in 1day kawai .

Ba kowane ke iya kwana cikinsa ba sbd tsadarsa domin akwai wanda yafi na 100k wanda dama yawancinsu se manyan attajirai ko 'yan siyasa ke kwana cikinsa.

Haka ya biya kudin kwana 7 Zarah da mamaki ta dubeshi batace komai ba Amma ga gidansu mezesa suzo hotel su kwana ?

Hotel ma  irin wannan me tsada haka meyasa Musayyet bayajin fidda kudi masu yawa yayi abu ne?

Let's go kawai taji yace mata ya rike hannuta sukai lifter har zuwa bangare na 3 suka fito .

Wajene na alfarma wanda seka rantse bame rayuwa cikinsa duk inda ka wuce sanyin AC ne ke ratsaka har zuwa room d'in daka za6a.

Room d'in  babbane ba abunda babu cikinsa kama daga toilets wajen cin abinci a kwauwame yake se wani hadadden bed wanda akwai tv jikinsa inkaso kai kallo zk fito da ita da remote kuma zk iya maidata ciki  yazama na kamar babu ita  ajikin bed d'in.

Carpet ne zagane a room d'in me round ko ina yaji kayan alatu dana kyalekyale se kujeru dk gefe waje daya da pillows d'in su

Zarah ta kalle shi da murmushi kan face d'in ta tace anan zamu kwa,,,,,,setai shiru shiko yai dariya ya janyota jikinsa ya shiga rage mata kayan jikinta yarage dg ita se best da mini pant.

Shima kayan jikinsa ya rage sannan yai waya yayi order cewan akawo musu abinci yafadi abinda za a kawo.
Duk cikin harshen larabci sk magana .

Musayyet yajanyota jikinsa yace bancika son zama waje daya ba Zarah tin ina yaro haka duk inda zani inaso wanda nakeso yakasance tare dani kamar ke d'in nan.

In zan tina rayuwata ko a cikin daji bana zama waje d'aya tin bansan gurare dayawaba har nazo nasani.

Ni mutunne me son ganin gurare daban daban nafiso nasan inda bansani ba Zarah .

Knocking yaji ya kalli hanyar door d'in ya lilli6e zarah sannan yatashi ya amso kayan yadawo ya rufe kofar.

A dining yaje kayan ya kamo hannunta suka zauna sk fara cin abinci.

Zarah tace so nake kabani labarin ka inason sanin kokai waye.

Kallonta yai murmushi yace zaki sani ne tinda muna tare yanzu zanje company ne na dawo ga kayan kallo nan """bazan wuce 1hour ba zan dawo karki damu .

Zarat tace to Allah ya kiyaye hanya .

Kiss yai mata sannan yasa kayansa yadauki key ya sakko kasa.

Bayan yafita zarah ta mike tsaye tana kallon window dk gefenta tana kallon yanda wajen

yakeda kyau ga korayen bishiyu  .

Tabbasa wannan  itace irin rayuwar datake muradi """itace rayuwar datakeso takasance tare da ita da wanda takeso Musamman da miji kamar Musayyet  mesonta me kula da ita Abun Alfaharinta.

Wayoyinta ta d'auka ta shiga saka numbers d'in dk d'ayar .

Kan bed ta haye sannan ta shiga kira

Kiran farko Ammi tafara kira alokacin Ammi tana kwance tanacin  kaji daga gefe kuma ga lemon kwakwa me sanyi yayinda malam  hadi zaune daya jikin kūjeran yana cin abinci.

Ba wayarkice ke karaba ? Cewar malam hadi.

Ammi ta aje plate d'in kan center tace itace kuwan """d'auka tayi yayinda tai sallama Zarah ta amsa tace ina kwana Ammi.

La Zarah ce mutanen kasar waje toya garin """"zarah tai dariya tace Ify lau ya kuke Ya babana?

Ammi tace kowa Ify ina balaraban mijin naki incede kuna zaune Ify?

Malam hadi ya kalleta  yace waike wace irin macace ne dan Allah  yanzu idan mijin na nanfa kice me?

Ammi ta kalle shi ta ya tsina fuska tace to meye aciki ba balaraban bane ?    Ai dan yayai kama dasune yasa nace haka .

Zarah tana jinsu tqi dariya tace yana Ify  bani baba mugaisa.

Ammi tace kafin na bashin inason gaya miki yakamata kisa yasemiki golds masu kyau da tsada acen """kinsan anan zasufi kyau da sauki a ganina.

Zarah ta dafe kai da hannu  cikin ranta kai Ammi .

Malam hadi ya amshe wayar yace zarah ya kuke ya zaman kasar ince de  ba wata matsala.

Zarah tace bakomai baba ya kasuwa.

Kasuwa Ify lau yanzu de inada yara wajen biyar kinsan nayi shaguna da kwantena wajen 7 kuma ana ciniki sosai .

Zarah tace Allah yasa albark baba .

Ameen Ameen ki dinga bugowa munajinki kinji ko.

To baba zandinga kira.

Sallama sukai batare daya kuma bawa  ammi wayarba duk da tason magana da ita.

malam hadi yace  yakamata ki kyale yarinyar nan  dan Allah kibarta  hankalinta ya kwanta waje daya karki sa mata kwadayin wani abu cikin ranta duk da nima de da farko kwadayin nabi harna aura mata Alhaj Sa ed.

Amma yanzu na sauya nagane ba abinda kwadayi ke haifarwa se wulakanci duk da bas ta6a yimana ba sema mutuntawa da darajawa  dasuke nuna mana.

amma aduk sanda kai nesa da kwadayin hannun abun wani tofa seyafi ganinka da mutunci da daraja""" ina gayamiki ne danki gyara halinki.

Tunda mutanan nan masu yine dakansa zakiga yaemata abunda yafi hakan """"dan Allah kisauya hali kinji ko.

Ammi tai shiru yayinda yafice yabarta zaune a nan.

Tai ajiyar zuciya  tace insha Allah  zan sauya daga yau Allah  yasa mufi karfin zuciyarmu amin

Zarah ta kalli wayar tace wai meya ammi take haka nifa banda tsarin naita cewa miji yaimin abu

yai min abu""" hakan takurane da matsawa kai""""""koda miji nada niyyar yai mk abu sanadiyyar bani bani dakake masa yauda gobr seya dena yaji ka ishe shi.

Tashi tayi  tai sallah sannan ta shiga kiran wayar Ayshan nigeria.

⚜BRILLIANT  WRTS ASSO🖊

👳🏻👳🏻👳🏻👳🏻👳🏻👳🏻👳🏻👳🏻

AURAN BABBAN

MUTUM

💃💃💃💃💃💃💃😊 MASOYA AKWAI DAD'I """"""   ngd muku sosai Masu comments  da masu kira   awaya""""" Hasana ina mik'o gaisuwa duk  da bansan kiba kirana kawai kikai d'azun a waya"""""" Allah yabar zumunci ka had'amu da masoyammu da gaskiya.

Allah  kabawa k'asarmu zaman lfy da kwanciyar me d'orewa """ya Allah duk wanda yake da hannu wajen tashin hankalin bayin Allah musulmai ya Allah munbarka dashi """""" kamaida musu duk wani mugun nufinsu zuwa kansu Ameen ya ALLAH👏🏻👏🏻👏🏻😔😔😔.

🅿48

So biyu wayar tai ringing Aysha na wanke wanke ta jiyo k'arar wayar ta taso da gudu ummanta

na shirin fita ta kalleta tace wai bazaki dinga abu a hankali bane ? Sunan an kusa auranki"""haka mijin idan yakiraki zai falfala kamar wacce aka biyo?

Aysha tai dariya tace kai umma """" umma tace ni sena dawo kyad'ora girkin """: to umma sekin dawo Allah yakiyaye hanya.
Ameen umma tace tai hanyar fita wanda seda ta karanta addu'ar fita dg gida sannan tasa k'afarta zuwa waje.

Aysha ta d'auki wayar wacce ta yanke da kira tai shiru tn kallon number """" nan aka sake kira Aysha cikin iya magana da mak'ale murya tace hello """
Jitai an kwashe da dariya Zarah tace wakike mak'alewa voice haka?

Aysha ta mik'e tsaye ta buga tsalle tace Zarah dama kece ?

Dariya zarah ta kumayi tasa juice abakinta ta sha sannan tai juyi kan bed tana murmushi tace nice wlh """ kalma ta farko d zanfara da ita shin kiyi hkr na mk lefi.

Aysha ta zauna tana dariya tace lefin me? Keni ba wannan ba wai kinada ciki kuwa nifa naji shiru.

Zarah tace kinga zaki farako toko cikin nan zaki siyon akasuwane ki mannan a cikina? Kullun maganari daya itace ciki.

Aysha ta kifa kanta kan bed ta soma dariya harda kwalla tace danasan inda ake siyarwa ai da tini sede ki ganki dashi .

Dariya sukai Aysha cikin zumudi tace kitayani murna nafa kusa aure nima nai mk lefi wayarkice idan na kira bata shiga """an de saranata yanzu befi saura 2months bikina ba.

Zarah ta bude ido tace iyyyeee lalle ne eh kyace kin min lefi amma fa nawa yafi naki .

Danni ayanzu harnayi wani auran ma munrabu da Alhaj sa ed.

Aysha ta dora hannu aka tace nashiga uku yanzu seda kikasa yarabu dake zarah """" wallahi baki kyautaba ni kinban haushi ma wlh""""yanzu wane soket d'in kika aura?.aysha tai maganar tana cuno baki.

Zarah sedata mik'e  zaune ta kyalkyale da dariya tace a a uban soket na  aura """" dariya aysha tayi tace maida wukar sorry dan Allah  wai da gaske kike?

Zarah tai dariya tace ina wannan guy dayazo tafiya dani wajen dinner da daddare/////   aysha tace wai handsome?  Zarah tace au sunan da kikasa masa kenan?

Dariya Aysha tayi eh man ai ya hadu ba k'arya sede mehassadine zece beba.

Zarah tai juyi sannan tace to shina aura.

Aysha tai murmushi  tace wlh ban yadda ba taya hk zata faru.

Nan zarah taita bata lbr tin dg farko har k'arshe aysha ta saki baki tana ta sallan lami  tace ikon Allah  kenan baya k'arewa""" Amma nai mk murna   kice ana nan ana soyewa dama irin mafarkinki kenan arayuwa Auran yaro dede ke ta yanda zakuci soyaiyarku.

Zarah dariya tayi tace Allah har ynz kunyarsa nakeji.

Aysha tace la amma kin ban ma haushi dama abun naki na cika bakine ?       Zarah tace a a wlh """ to in bahakaba ai kema seki nuna masa cewa kina sonsa kuma shine dede ke.

Zarah tai ajiyar zuciya tace yanzu yaushe ne bikin?

Eh  nan da wata 2nefa.

Zarah tace ai innazo sati 2 zanyi.

Dariya aysha tayi tace eh ai kinsan ni barinki  zanyi kiyi haka kurun kinsaba masa da jikinki yawani zauna harna 2weeks bake.

Kinji kiko""" cewar zarah"""   eh ai gaskiyane

Nan aysha ta bata labarin Naseer da yanda akai sk had'u """ zarah tace amma shine baki

fadamin ba a she tin ran daurin aurena?

Aysha tace shiyasa nace namiki lefi.

Zarah tae nima namiki semu taru mi hkr duka.

Hakane zamike chart ai """ ah sosai ma zanyi saving ynz.

Sunjima suna waya dg qarshe sukai sallama """

Musayyet se yamma ya dawo ya biya wani mall  ya jido mata dogwayen riguna masu uban tsada  da kayan makeup dana ciye ciye ya taho dasu

Wanka take tin dazun kamar me canja skin""" motsi kawai taji hakan  yasa ta tsorata tana zare ido.

Shiko Musayyet kasancewar yanada d'an katin nan wanda ake karawa jikin kofa shiyasa ya shigo batare data saniba .

Toilet d'in ya bud'e ya shiga ya ganta zaune cikin hadadden bahon wanka kunfa duk ta cika bahon se kamshi yake """ido ta rufe yai smile sannan ya hau cire kaya.

Tsulun ya shiga ciki ya jawota  yana  wanke mata wuyanta """""":   tai murmushi kanta na k'asa yasa hannu ya dago kanta yai mt kiss a goshi yaci gaba dayi mata wanka.

Bayan yagama ne yace setai masa shima"""""" kai ta girgiza masa ya d'an had'e face """Zarah tai saurin matsowa kusa dashi tana girgiza kai tazo daf da kunnensa tace karkai kuka zan maka .

Kallonta yai yn murmushi bece komaiba tafara wanke shi yayinda ya kwantar da kansa bayan bahon yanajin yanda tk wanke masa sassan jikinsa  cikin wani salo me dadi.

Jiyai kawai tace kai "yai saurin bud'e eyes shima yana fiddo ido zarah tai surin fitowa dg bahon shiko dariya yakamayi yana shirin kamota.

A shewer ta karasa  wanke jikinta ta fito tn maida numfashi.

Musayyet yana kwance cikin bahon wankan lokaci lokaci yana tina abunda yakasance yanzun.

Wato tana cikin wanke  shine hannunta yai k'asa nan ta ta6o babban waje shine tai saurin fitowa.

Dariya yayi cikin ransa kai Zarah kenan.

Zaune yaganta kan bed ta kimtsa a  daya dg cikin kayan daya siyo mata """ tayi kyau sosai face d'in ta se Annuri tk.

D'aure  yake da tawol iya k'ugu yq zauna daf da ita ta kalleshi setaga shima ita d'in yk kallo tai saurin kasa da kai.

Yai dariya ya kwanto da ita jikinsa ya rungumeta  cikin voice kasa kasa  yace dn Allah  kidena jin kunyata haba hubby na.

Smile tayi sannan tace rufe idonka """ Ahankali Musayyet ya rufe idonsa jiyai kawai ta masa kiss a mouth ta rufe idonta don kunya .

Idonsa ya bud'e  yai murmushi yace ngd  haka nakeso """kisani cewa ayanzu munzama daya kinzamani nazama ke ,,,,  batun yanzu ba nakejin ki araina wlh inasonki zarah banajin zan  iya

nisa dake kona tsawon kwana dayane bazan iyaba .

Smile  tayi cikin murya tajan hankali tace nima inasonka Ina ftn Allah yabarmu tare

Ameen yace suka tashi zaune yace to a gyarani .

Dariya tayi sannan tashiga shafa masa bodyCream me tsadar gaske wanda kesa fata kyau  da shek'i.

Bayan sungamane tace naga ka siyo wasu kayan dan Allah kadena kashe kudi da yawa haka """""""""""""...........    Musayyet yai murmushi yace meye  abun kashe kudi anan banaso kede kawai kimin addu a shine kawai naki.

Murmushi  tayi yai smile takeaway  yajawo ya aje kan dining ya fito da juice da wani gasassen kifi yafara bata abaki itama tana bashi..

Bayan sungama cin abincin fita sukai zuwa mike k'afa yayinda suna fita ma aikatan gun suka shigo room d'in  suka hau gyara suka sanya komai  sabo  suka wanke toilet  tsaf ""sabon sabulun wanka suka aje se wani soson wankan sabon brush da  oralb suka sanya se Airfreshner suka turara room d'in  da turarukan wata irin nasu masu kamshi suka jawo suka kulle.

Haka ka idar  su take inde bako ya fita dg room d'in sa to sukan shigane su sake komai sabo sugyarashi .

⚜BRILLIANT  WRTS  ASSO🖊

👳🏻👳🏻👳🏻👳🏻👳🏻👳🏻👳🏻👳🏻

AURAN   BABBAN

MUTUM

Crtng And Wrtn By

UMMMEE MUKHTAR🎁

🅿49

Wani lambu suka samu suka zauna wanda aka gewayeshi da kujeru na Alfarma dg kusa dashi wani babban swimming pool ne wanda akai masa zane na heart ruwa kwance cikinsa garai garai me sanyi dashi.

Musayyet ya zaunar da Zarah dg d'aya daga cikin kujerun dk zagaye agun dede saitinsa yana kallonta """"" yana kallon yanda ta k'ara haske da murjewa daga 'yan wannan kwanakin ,,,, eh lalle zama yakamashi anan inde Zaransa zataji dadin hakan.

Zarah na kallon yanda yakafeta da ido murmushi kawai tana kallon kallon gefenta taname wasa da k'aramin mayafin rigar dk mak'ale a wuyanta wanda tai rolling dashi.

Smile yayi lokacin dayaji phone din sa na ruri nan ya dauka ya mike tsaye gamida zura hannunsa cikin jeans din dk jikinsa yana amsa wayar.

Ok shikenan dady nan da kwana 7 ne tafiyar? To dady insha Allah zani """ a a my son nasanka bakason zuwa spain bansan meye dalilinkaba kode har yanzu k'yank'ýamin nasu kake?
.dariya Musayyet yayi yana kallo Zarah ya daga mata gira tai murmushi "" yace no Dady ai yanzu ma girma banajin tsoron komaı.

Hmmm Dady yai murmushi yace shikenan seka shirya komai na tafiyar daga nan zuwa lokacin
.

Bayan sungama wayar ne yadawo ya zauna yn kallonta ya shafa kai yace hubby na tafiya zanyi yanzu dady ke sanar dani zaki iya zama ke d'aya kuwa.

Zarah jitai gabanta ya fad'i ta sunkuyar dakai tana  maida k'walla  wanda ke shirin zubowa.

Tasowa yai ya durkusa kan grass  wacce ke malale agun ya kama hannunta  yana shafawa yace is ok karki damu wasa nk miki""" taya  za ai nayi tafiya nabar rayuwata kinsan hakan baze yuwuba duk inda zani  kina tare dani  kamar yanda zan kasance tare dake.

Se nan ta d'ago kai tana murmushi  ya lek'a idonta yana smile  yace  sarkin kuka .

Smile tayi kawai batasan meyasaba bataso yi nesa da ita kwata kwata tariga  data saba da jikinsa me laushi a 'yan kwanakin nan batajin zata iya nesa dashi.

Yace Zarah kinsan Manbila?

Kai ta girgiza masa yai murmushi yace nan ne asalin garimmu  cen cikin wani daji wanda ba mutane dayawa cikinsa """"  Kwata kwata bukkar dake cikin dajin batafi guda 7 ba wanda yawancinsu kiwone aikinsu """ basu cika zama waje d'ayaba sede  dg wannan gari zuwa wannan gari .

Sunan mahaifita Shatu wanda sedana girma nagane duk me suna shatu ana nufin Aisha kenan.

Babana shine Malam Musa wanda tinkafin nai wayo Allah yai masa rasuwa .

Se yaiyena guda 2 duk mata wato Mulabi da kuma Sa 'ade.

Allah ya Alabarkacemu da shanu masu yawan gaske wanda duk rugar tamu bame yawan shanun mahaifina koda yk daka d'anne sukafi na makotammu """      Tin  in yaro jinina yafi haduwa dana yayata Mulabi wato momyn Khairat      """"""  Musayyet ya kalli  Zarah  yaga ta zuba ms ido tana kallonsa sotake kawai taji yanda  akai sukabar garin.

Tai kasa da kanta  tace Allah  yajikan baba yasa yahuta

Ameen   Musayyet yace yana me kallon gefensa .

Yace tin ina shekara uku nasaba da shiga cikin shanu wanda ba abinda sukemin haka na maidasu abun wasana """kullun dagari ya waye Allah  Allah nk na isa gunsu yayinda anty na ke dorani kan wata karamar saniya tana  zagayawa dani.

Bishiya kam yanda kikasan dan biri da minfita kiwo da zarar an tsaya huta k'afa ko rangadi ko an tsaya dabbobi su sha ruwa senai saurin hayewa kan bıshiya hk zasuyita nemana harsena musu gwarancina cewar gani anan  sannan zasu sakko dani.

Zarah dariya ta kufce mata tasa mayafi ta kare face din ta ya kamo hannun yana daria yace dariyar me kike?

Batace komaiba illa wata dariyar data sk kufce mata yasake  matseta jikinsa yanaiwa wuyanta kiss.

Zaki fada kosena sake abin jiya?
.da sauri ta tsaida dariyar ta turu  baki tace  toba kaine kace wai kamar dan biri ba.

Shima dariyar yayi yace eh man amma yanzj banajin zan iya wannan tsalle tsallen.

Akwai wasu mutane wanda ba Musulmai bane duk inda sukasan akwai wata k'aramar ruga sukan kai mata harine  sukashe  su kuma su debe duk abinda suke dashi tin daga  kan dabba zuwa  abincin ci.

Hakanne yasa bayan rasuwar mahaifiyarmu yazamana cewa semu  uku muka rage .

Watarana cikin dare wa 'yan nan mutanan suka kawo hari wanda tin daga nesa mukafarajin ihunsu kamar na tsuntsaye wani tsohone ya farga da hakan cikin sauri yai inkiya wa mutanen rugar tamu kafin kame meye sun shigo cikin dajin .

Nan suka fara aikin zalincinsu wanda alokacin yaiyena bacci suke nina hau tashinsu.

A gigice babbar yayammu ta farka ta kaiwa Mulabi duka itama ta farka cikin kuka ta hau sheda mt abindake shirin faruwa .

Jikinsu na rawa  suka hau kuka duk da yarone ni amma nai musu inkiya cewa dasuyi shiru kar ajisu.

Ta cikin bukkar suka lek'a  nan suka hango har sunnawa wasy bukkoki wuta sun kwashe abinda ke bukkar.

Cikin kuka naga sun hau keta bukkar tamu ta baya da wata k'aramar  wuk'a da alamu hanya sukeyi.

Ni momy tafara sawa sannan waje sannan sa ade ta fita itama momy ta fito dakayr jikinsu duk ya kuje da zanar bukkar  kasancewar su farare nan da nan jikinsu ya hau jini kuma yai ja jawur .

Da sauri momy ta koma ta dakko wani kullin k'yalle wanda daurin kudine cikinsa ,,garin fitowarne tsautsayi yasa ta soke da wannan  zanar bukkar a cikinta tasa k'ara  sa ade tai sauri janyota ta rungumeta ganin yanda jini ke zuba ta gefen jikinta """ dankwalin kanta tasa ta daure mata cikin sannan ta goyata ni kuma tana rike dani muka nausa cikin daji """" ga uban duhu gashi dare yayi ko gabammu  bama gani haka mike tafiya .

